An dauko wannan littafi daga shafin www.arewanovels.com.ng ku ziyarci shafin na www.arewanovels.com.ng domin samun kayatattun littatafan hausa kama daga kan na yake yake dana soyayya

Marubuci ko marubuciya zasu iya turo mana da littatafansu mu dora masu a shafinmu kyauta don masoyansu su rika Downloading a online,

Sannan marubuta zasu iya turo mana da tarihin rahuwarsu da tarihin rubutunsu, dama sharhin littatafansu don masoyansu su gani kuma su karu da hakan
Domin turo mana da littafi ko tarihin rayuwar marubuci ko marubuciya sai ayi mana magana ta whatssap da wannan nambar +2347032707179

A lura dakyau - kyauta muke saka littafi a shafinmu bama amsan ko sisin marubuci, duk wanda ya amshi kudinku da sunanmu babu ruwanmu,

Alura dakyau - manazarta bama tura littafi ta private ku dena binmu private kuna neman mu tura maku littafi, duk mai bukatar littafi yaje website namu

Alura da kyau - Littatfanmu suna fitowa cikin manhajoji uku ne PDF,TXT da DOC amman munfi amfani da PDF da TXT masu amfani da wayar android ko tablet ko computer zai fi kyau ku riga dauko PDF da DOC

Masu amfani da kananan wayoyi java ko mara java TXT zakuna zaba don shine daidai wayarku

This hausa novel was uploaded and downloaded from www.arewanovels.com.ng
You can download more hausa novels there
Also you can send us your novel to upload it in our website for your fans to download it online
It is free we do not charge for uploading novel
Also if you are an Author be it online or Non online you can send us your biography including your book summary,commentary and others via this number +2347032707179 its free we do not charge for our services

Note that - we do not charge for our services we uploaded novels and posted biography free, any person that collect your money in our name is your fault do not blame us

Note that - pls readers stop calling us and be asking us to send you a novels we are not sending novels through whatssap or private our novels is public at any day, any time you can visits our site and download it

Note that - our ebooks came as PDF,TXT or DOC format but the popular format are PDF or TXT, those with android or tablet or pc we suggest you to download PDF or DOC
those with java phone or non-java phone we recommend you to download TXT

—
WHATSAPP NO:
+2347032707179

AL'AJABI part 1
Tsaye yake ya dafa tebirin dake gabansa tare da rankwafawa kansa na kallon tebirin dake gabansa, kallo daya zaka yi masa kasan a cikin damuwa yake.
Ya dago kansa tare da matsawa yaci gaba da takawa ya fara safa da marwa a cikin faffadax ofis din nasa, tsawon lokuta ya shafe yana kaiwa da komowa ya rasa me ke masa dadi.
A tsayen ya zura hannunsa ya zaro wayarsa dake al'jihu ya lalubi lambar wanda yake son kira tare da karata a kunnensa ya taka a hankali izuwa kan kujerarsa ya zauna, hannunsa daya na rike da wayar yayinda dayan hannunsa ke dafe bisa tebirin dake gabansa.
Hello!! ya fada dai-dai sanda aka daga wayar sannan ya dora da cewa " Ranka ya dade yarinyar nan fa har yanzu bata zo ba ina tsammanin ma ba zuwa zata yi ba, gaskiya na gaji ga yamma na dada yi kuma na gaya maka uzuri gareni ga yamma na dada yi."
Cikin rarrashi wanda ake yiwa wayar yace " Ahmad kayi hakuri ta taho go slow ne ya riketa amma yanzu zata karaso."
Ahmad din ya kara bata rai ya kauda wayar daga kunnensa ya ajiye wayar bisa tebirin dake gabansa ya kwantar da kansa jikin kujerar ya zubawa kofar shigowa ofis din ido, sai daya shafe wasu mintuna ashirin din babu alamun wani zaizo sbd takaici runtse idonsa yayi kamar barci yakeyi sai dai a zuciyarsa 2nanin irin fadan dazai rufeta dashi kawai yake.
As-salamu-alaykum.
Wata zazzakar murya tayi sallamar data saka Ahmad saurin dago kai tare da gyara zamansa yana me kallonta har izuwa sanda ta zauna tana me fadin "gani na iso".
2nanin da yake tayi a baya sai yayi saurin kawar dashi domin kallo daya yayi mata yasan tafi

karfin wulakanci ko a tozartata ba karamin kwarjini gareta ba, zunzuru2n kyau kuwa ba'a magana lallai Allah yayi halitta.
ya fada a zuciyarsa.
Amma dai kinsan kin bata min lokaci ko??
ya fada yana dubanta.
ba tare da alamun nadama ba tace " Eh nasani ".
To me yasa?? koda dai ance wai go slow ne ya rikeki??
Ya tambaya ba tare daya dubeta ba shima.
Tayi saurin girgiza kai tace " gaskiya karyane hasalima ban taba hawa titi fayau irin yau ba, ni din ce kawai ban taba hawa titi fayau ba motoci irin yau ba, ni din ce kawai ban gadamar fitowa da wuri ba."
A karo na biyu ya sake dubanta da sauri ya danyi shiru na dan lokaci sannan ya kawo gwauron numfashi ya gyara zama yace " Ance min in jiraki za'a miki dan interview na yan mintuna kuma a daukeki aiki a baki ofis kai tsaye, koda bansanki ba amma nasan tabbas wanda ya tsaya miki babba ne don ban taba ganin inda akai hakan ba sai akanki don wasu da wuya suke neman aikin basu samu ba wata kila hakan ne yasa kike wani ji dakai kina gadara aikin ma ba wani damunki yayi ba."
Ta tsuke baki sanda ya kawo karshen zancen nashi tace " Gskyne ba damu na yayi ba kusan ma ince maka tilastani akai sbd ansan nice zan taimaka muku ba kune zaku taimaka min ba, batun wanda ya tsaya min kuwa koda a fadar shugaban kasa ya nema min aiki ba wanda ya isa ya hana bare nan."
Tayi nuni da ofis din a wulakance.
Ahmad ya sake binta da kallo a zuciyarsa yace " Wannan tafi ni bala'i."
Ya gyara zamansa tare da jawo laptop din dake gabansa ya mayar da hankalinsa gareta jim kadan ya dago kai yace " Meye sunanki?? "
Kanta na duban tebirin dake gabanta tace " HUMAIRA ".
ya danyi shiru kadan kamar me sauraron kara jin wani abu daga gareta, jin tayi shiru yasashi ture

laptop din daga gabansa ya dubeta yace "
Yakamata kiyi min adalci, kin bata min lokaci a zuwanki amsa tambayar ma sai kin sake bata min wani lokacin??"
Au wai kana nufin full name?? To sunana HUMAIRA ISMAIL.
Ta fada tana me kallonsa.
Ya jawo laptop sanda yayi tsaki kasa-kasa.
Meye level din karatunki??
Ta amsa da cewa " Masters degree ".
Yayi saurin dubanta cikin mamaki a ransa ya sake maimaitawa ( masters ) tab!!!!!
Wacce jami'a??
Ya sake tambayarta kansa nakan laptop din.
Ta dan kauda kanta kadan tace " oxford university- ENGLAND."
Bai san sanda ya sake dubanta ba cikin mamaki,
A yarinya dole kiyi girman kai!! Ya fada a zuciyarsa.
Yayi saurin kauda kada ta fahimci halin da yake ciki yace " kinzo da takardunki ne??"
Babu bukatar zuwa dasu 2nda ba maular aiki nake ba dazan rinka yawo da takardun makaranta.
Bala'i!!!! Lallai wannan tafi ni masifa.
Ya danyi shiru zuwa jimawa yace " last question!!
Relationship??"
Tayi shiru kamar bata jiba ya sake maimaitawa da hausa da fadin " budurw, bazawara ko matar aure?? wannan abu ne da dole a sani a duk inda mace zatai aiki a duniya.
Fuskar Humaira tayi saurin canjawa izuwa yanayi na damuwa tace " Don Allah kasa UNKNOWN kawai."
Ahmad ya hade rai cikin takaici ya shafa kansa "
Wai ke wace irin mutum ce don Allah ?? Ya kike meman kisani ciwon kaine?? baki ma san ke budurwa ce ko bazawara ko matar aure ba?? "
Tayi saurin gyada kai tace " Eh bani da tabbacin zama daya daga cikinsu."
Ahmad ya mike cikin tsawa yace " wallahi karyane hakan baya taba yiwuwa dole a samu kina daya daga cikin wadannan azuzuwan ".

Ta mayar masa da martani da cewa " ba wani dalili da zaisa inyi maka karya 2nda ba aljanna zaka bani ba don haka karka kara karyataniakan abinda baka sani ba.
Ta dubeshi hawayen dake idonta suka yi gaggawar zubowa ta dora da cewa:
" Na rantse da Allah idan nace maka ni budurwace nayi karya!! Idan nace maka ni bazawara ce nayi karya!! Haka idan nace matar aure ce ni karya nake!! Ni kaina bansan da sunan da zan kira kaina ba.
Ahmad wanda fusata ta sashi mikewa yayi saurin komawa ya zauna idonsa ya zaro sbd mamaki, da AL'AJABI zuciyarsa ta fara sake-saken tayaya ma hakan zata faru??????????????????????????
???????
AL'AJABI part 2
NA A.A. muhammad
with==>Aßu Fer'ezerh
Ahmad yaci gaba da kallonta kawai har yanzu mamaki ne cike fal kuma rubuce a fuskarsa,
Abinda ke yawo a zuciyarsa shine:
Babu alamar wasa a tare da ita, hasalima hawayene ke zuba bisa idanunta a halin yanzu kuma gashi ta rantse, Tabbas hakan na nuni da cewa har cikin zuciyartane abinda take fada.
abin AL'AJABI mafi girma da kunnuwansa suka taba jiye masa kenan.
Tunani daya da yayi wanda ya kore 2nanin da yakeyi a baya shine: To kodai don ni namiji ne yasa ban fahimci abinda take nufi ba??
Tabbas shine dalilin.
Ya bawa kansa amsa dai-dai sanda ya dubeta tare da zaro wasu takardu dake gabansa ya dora a gabanta yace " Yanzu dai shikenan kiyi hakuri ki daina kuka ga kundin takardun da kike bukata a aikinki bari nasa masinja yayi miki jagoranci izuwa ofis dinnaki, daga yau kece babbar me kula, da adana bayanai na wannan ma'aikatar ALLAH YA TAYA RIKO."
Yakai karshen maganar dai-dai sanda ya waiga tare da kiran sunan masinja, BALA!! BALA!!!
Da sauri ya karaso tare da dukawa yace

"Yallabai".
Ahmad ya dan kwantar da kansa bisa kujerar da yake zaune yace " Kuje da ita ofis no: 11 ka hadata da sakatariya zanyi mata waya."
Da sauri bala masinja ya amsa da " To Yallabai "
Ya wuce yayi gaba.
Humaira dake zaune ta mike ta jawo jakarta wadda ta dade da dorata bisa faffadan tebirin dake gabanta, ta debi takardun da Ahmad ya bata ta zuba a ciki tare da gyara zaman bakin glass din dake da fadin rufe idonta daya matukar kara mata kwarjini.
Ta dan bishi da kallo kawai ta juya ta nufi kofar fita daga ofis din, Yayi saurin cewa " Koda ba yanzu ba ina fatan na sami labarin rayuwarki wanda ta yiwu ya warware min rudanin dana ke ciki."
Tayi saurin dakatawa tare da dawowa da baya a hankali tace " Idan har ba kana yin haka bane don ka gano hanyar karya zuciyata ba to na rokeka ka bari, ka kalleni a humaira kawai karka takura wajen binciken wacece ni sbd ba abune me samuwa a wurinka ba, Ta dan kara daga muryarta tace " Bakina bazai taba iya furta labarin daya faru dani a baya ba kamar yadda kwakwalwata ba zata juri tunano hakan ba, idan kana son mu zauna lfy dakai karka kara taso min da wannan zancen."
Takai karshen zancen cikin tsawa a dai-dai lokacin data canja gaba daya kamar ba ita ba.
Taja da baya ta fice da sauri.
Ahmad ya bita da kallo lkc guda ya mike izuwa tagar ofis din ya hangeta ta glass kai tsaye wata tsaleliyar mota kirar TOYOTA PRADO ta dosa ta bude motar ta shige, motar tata tabi bayan tsohuwar HONDA CIVIC wadda bala masinja keja don yi mata rakiya.
Ahmad ya kauda kansa daga wurin ya fara takawa a hankali cikin ofis din, Yarinyar nan fa ba karya takai tayi takama ko gadara, kallo daya yayiwa motarta yasan ta fito ne daga gidan masu akwai, to amma meye mummunan abinda ya faru da rayuwarta har yasata shiga yanayin da take

ciki?? menene musabbabin hakan??.
Abin nema ya samu don haka wlh sai na sani kota halin kaka.
Ya fada a fili, ya juya ya rufe laptop dinsa tare da jawo bakar jakarsa ya zirata a ciki, jakar tasa na hannunsa yayi waje.
Kai tsaye motarsa ya nufa yabi tsaleliyar hanyar data nufi kudu, a ransa ya darsa cewa ya fasa zuwa inda yayi niya 2nda yamma ta riga tayi.
Duk da sanyayyar wakar mawaki justin bieber dake tashi a hankali cikin motar tasa baisa ya manta da abinda ke ransa ba.
Mintuna Ashirin ya kwashe ya gangaro cikin katafariyar unguwar tasu, rukunin gidaje na NEWCLAX QTRS. tsararriyar unguwa ta gani da fada.
Worn daya yayi a bakin tafkeken koren gate din ya fara budewa a hankali bisa jagorancin wani siririn matashi wanda yayi saurin cewa " sannu da dawowa ".
Ahmad ya gyada kai tare da fadin yauwa.
Ya wuce da motar yayi parking dinta a harabar gidan ya wuce izuwa cikin, shigowarsa falon keda wuya yaji kyas!! Alamun daukar hoto, yar kyakykyawar budurwar ta tuntsire da dariya tace " gaskiya yaya hoton nan yayi kyau, bari a kara maka daya."
Ya dan harareta kadan yace " ke baki da wani aiki saina daukar hotunan mutane a waya ko??"
Ya karasa ga daya daga cikin kujerun dake zagaye a katafaren falon, momi dake zaune kanta na kallon TV din dake jikin bango ta juyo gareshi tace " Ahmad an dawo kenan??"
Wallahi momi sai yanzu,
Ya fada cikin ladabi.
Dai-dai lokacinne saudat ta dire farantin juice dake hannunta ta tsiyayo lemon a dan karamin kofi ta mika masa, Ya amsa tare da cewa " Thank U my blood sister, yau dai kina da kirki ".
Ta juyo tace "yau kawai??"
Ya gyada kai yace " iya yaune kawai ".
Ta juya ga momi dai dai sanda ta karasa ga kujera ta zauna tace " momi kinji shi ko??".

Momi ta mike tare da cewa "zaku fara surutun naku kenan? to bada ni ba bari na shiga ciki lokacin sallah ya gabato."
Shigewarta sashin nata keda wuya Ahmad ya dawo kujerar da saudat ke zaune yace " yauwa ina da tambaya watakila keki sani don nidai nayi iya tunanina na kasa ganowa amma fa gsky zaki gaya min pls".
Tayi murmushi tace " fadi muji idan na sani ".
Ya gyara zama yace " Tayaya mace zata zama ba budurwa ba, ba bazawara ba, kuma ba matar aure ba?? Sannan da wane suna za'a kirata?? "
Saudat ta danyi shiru can tace " waye yayi maka wannan tambayar?"
Ya girgiza kai tare da cewa " ba ruwanki kawai ki amsa min idan kin sani ".
Saudat ta kyalkyale da dariya tace " Amma yaya anyi saurin juya 2naninka daka kasa gano amsa me sauki irin wannan, mace na iya zama ba bazawara ba, ba budurwa ba, ba matar aure ba IDAN..........!?¿¿
Good morning....
*** AL'AJABI PART 3 ********
.
Hakan na iya faruwane kawai idan fyade akayi mata, kaga ta tashi daga budurwa, kuma ba bazawara bace sannan ba matar aure ba. Ahmad yayi shiru cikin salo na nazari jim kadan y girgiza kai yace ' gaskiya baki fada dai-dai ba wacce aka yiwa fyade ai ta zama bazawarako??" Saudat tayi shiru kawai tabishi da kallo, tabbas ya ta gsky kuma ba dai-dai ta fada ba. Ahmad yadan harareta kadan ya tashi izuwa kujerarsa yace " ke dama idan ba danna waya ba me kika sani??" Saudat tace " to ai ko ba komai nayi kokari 2nda nayi tunanin abinda kai baka yiba." Ahmad ya kauda kai yace " kinyi tunani amma useless ne ". Tabishi da kallo tace " kasan abinda za'ai? ". Ya girgiza kai alamar A'a.
.
Tace "bari mu tambayi momi 2nda ita tsohon hannu ce ta yiwu ta sani sai ta fada mana," Ta yunkura da nufin kiran sunan MOMI, Ahmad yayi

saurin dakatar da ita yace " KE! rufa min asiri, bar don Allah. " Ta kwantar da kanta jikin kujerar ta kyalkyale da dariya tace " Amma dai yaya duk sanda ka samo wannan amsar don Allah nima ina jira sbd ina son nasan yadda akai hakan zata faru don nidai ina ganin da kamar wuya....." Ahmad ya mike rike da jakarsa yace " kada kiyi saurin karyata abinda baki sani ba, kiran salla ake bari na shiga ciki nayo alwala. " Tabishi da kallo kawai har ya shige dakin nasa, ta juya ta kwanta bisa doguwar kujerar tare da cigab da danna wayarta.

.

*********** ***********

.

*** BAYAN SATI GUDA ***

Zaune take cikin faffadan ofis din ita kadai ba tare da kowa ba, babu alamun motsin wani tsit ofis di yake sai dai na'urar dake nuni da shigowar sako dake kadawa a hankali lokaci zuwa lokaci. laptop ce a bisa tebirin dake gabanta gefe guda takardune da files tuli da ita kanta bata san adadi suba. Sai dai gaba daya hankalinta da 2naninta ba akan aikin dake gabanta yake ba, uban tagumi kawai ta zuba da dukkanin hannayenta biyu, glass din data saba sakawa a idonta ajiye yake a gefe wanda hakan ya fito da hawayen dake zubawa a idanunt a zahiri. 100% na hankalinta ya tafi ne ga karanta wasikar jaki, koda ba'a fada ba tabbas abinda take tunani nada alaka da wani matsanancin yanayi da take ciki. uk da na'urar dake huro iska tako ina daga sassa ofis din amma hakan bai hana ta hada wani zazzafan gumi ba wanda ke ketowa daga sassan jikinta, hadewar da gumin fuskarta da hawayen dake kwaranya daga idonta suka yine yasa suka jika takardun dake gabanta sharkaf.

.

Nisan da tayi yasa bata ji shigowarsa ba duk da sallamar da yayi ta kwalawa, Ahmad yayi turus a gabanta yana dubanta kawai dai dai sanda fuskarsa ta canja daga murmushin da yakeyi, ya zauna a kujerar dake fuskantarta sai dai har yanx

bata dawo hayyacinta ba bare ta fahimci cewa wa ya shigo inda take, da alama bata ma san a inda take ba. bayan ya gama yi mata kallon AL'AJABIN ne kum ya kira sunanta. HUMAIRA hade da dukan tebirin dake gabanta. Firgigit! tayi tamkar wacce ta tashi daga barci, tab inda take da kallo kamar wacce ta ganta a sbn waje. Lokaci guda tayi kokarin goge hawayen dake idont ta kakalo yake ta maye gurbinsa dashi tace " Ah....Ahmad yaushe ka shigo??" Ya dan bita da kallo yace " Humaira kukan me kikeyi??" Tayi saurin girgiza kai tace " kuka kuma? ni... ba kuka nake yi....ba." Ahmad ya danyi guntun murmushi yace " Humair a rayuwa damuwa bata taba buya domin ita abac da ba a zuciya kawai take zama ba rubutu takeyi da manyan baki akan fuska wanda kowa sai ya gani, kuma koda ma tana buya to ta yiwu girman taki damuwar ta wuce a boyeta don da zata boyu da kin boyeta. Ya rankwafo da kansa gareta yace " Me zai hana bani dama nasan wani abu a rayuwarki, ta yiwu in da hanyar taimakonki koda da addu'a ne." Idan kana yiwa Allah ka daina yimin wannan maganar ba wani dalili da zaka damu sai kasan labarin rayuwata, Aikine kawai ya hadamu dakai k tsaya a iya haka ko don tsare mu2ncinka a idona. Ahmad ya daga kafadarsa kadan yace " 2nda ba zaki fada min ba shikenan, dama nazo ne na san dake gobe muhimman kayan aikinki zasu karaso saiki shirya." ya mike tare da cewa " see U next time ".

.

Ahmad!! Ta kira sunansa dai dai sanda yake gaf d ficewa, ya tsaya cak a hankali kuma ya dawo izuw gabanta. Ta dago kai tace " Don Allah kayi hakuri kayi min uzuri kwakwalwata ce ba zata juri tuno dukkan abinda ya faru dani a baya ba, amma ta yiwu wat rana ka sani." Ahmad ya zauna bisa kujera yace " Humaira wasu lokutan kunshe abu a rai cuta ne furtashi kuma warakane, yana da kyau na rike wani hujja koda guda dayane wadda zan rika nayi miki uzuri idan na ganki a yanayin dana ganki yau.," Hawaye suka sake gangaro mata

idanunta suka bude karrr tace " Tunda uwata ta haifeni ban taba ganin mutum mara yarda ba irinka, baka taba yiw mutum uzuri? kai kawai abinda kake so shine a ranka?? To bazan fada maka ba, tunda baya cikin sharadi abinda dole sai ka sani kafin ka zauna dashi, idan ka kara yimin wannan tambayar ba zaka kara ganina ba har abada. Akan me?? Ta fada da karfi sannan ta dora " Na zabi nayi aiki ne badon kudi ko don na samu wani abu ba sbd nafi karfin wannan, sai don ina tunanin hakan zai rage wani yanki na damuwa idan kuma kace takurata zakai kake bijiro min da wata damuwar abu me sauki na hakura." Takai karshen doguwar maganar tata da ajiyar zuciya. Ahmad yace " Nida kike ganina mutum ne me so samun labarai musamnan na al'ajabi, daga cikin labaran dana samu akwai a 2nanina naki shine za zamo na farko a ban al'ajabi, baki da wani zabi dolene nasan labarinki a yau." yakai karshen maganar cikin daga murya. Lokaci ta kara sauyawa ta hade rai ta kara fusata gami da harzuka ta kauda kanta domin ta gama zuwa iya wuya, Dame wannan mutumin yake takama daya isa yayi mata dole. Ta mike ta rufe laptop din dake gabanta ta jefa masa mukullin ofis din ta jawo babbar jakarta ta rataya cikin tsawa tace masa " Don ina aiki dakai ba yana nufin ka cutar da kwakwalwata bane, idan badon na kaskantar da kaina ba kai nafi karfin ka min dole wlh. Ga mukullinku nan tafiyata itace mafi sauki daga wannan matsin lambar taka.
.
Ta ture kujerar kusa da ita cikin sauri ta nufi kofar ficewa. Ahmad ya jawo mukullin ya rikeshi a hannunsa cikin sauri ya waiga kafin ta fice yace " Ba wani abu bane idan kin tafi hakan shine ma ya tabbatar min da mummunan zargin da nakeyi akanki." Duk da batai niyya ba amma sai da tayi saurin waigowa duk da cewa daf take da ficewa. Ahmad ya juyo sosai ya dora da cewa " Na yarda da cewa ke MUGUWA CE, tabbas ke ba mutuniyar kirki bace, a rayuwarki babu komai sai ta'asa da rashin kirki, na tabbata wani mummunan abu

kika aikata wanda yake bibiyarki kuma ya hana miki kwanciyar hankali......" Ya dakata da maganar yana kallonta. Idanunta suka zaro kamar zasu fado 'iiihhhhhhh!!!! bakinta ya fada dai dai sanda ta rike bakin nata, zuciyarta ta fara saka mafi munin maganganun da aka fada mata, lokaci guda kwakwalwata ta gaza jurar amsar kalaman, kanta yayi nauyi tayi saurin dafeshi, idanunta suka fara juyewa wanda yazo dai dai da sanda kafafuwanta t gaza daukar ganga jikinta, cikin sauri kwakwalwarta ta tuno mata abinda yace......

.

Na yarda da cewa ke muguwa ce, tabbas ke ba mutuniyar kirki bace, .......... na tabbata wani mummunan abu kika aikata daya hana miki kwanciyar hankali...... Dai-dai lokacinne ta karasa sulalewa kasa cikin yanayi na suma.... Wai wai wai wannan al'amari akwai rikici.

.

Kubiyoni anext..

Tsaye yake kofar dakin kula tare da yin aikin gaggawa na asibitin yana kaiwa da komowa, mintuna talatin kenan da kawowa kuma likitoci suka hau aiki amma ba wani bayani har izuwa yanzu.

Zuciyarsa nata yi masa sake-sake kala-kala, me yasa zaiyi haka?? Don me ma ya ma zan takura akan abun da bai shafeni ba?? Kada fa nayi silar kashe yar mutane ko na jawo mata w...........

Hango fitowar likitan daga dakin da yayi ne yasa ya dakata daga zancen zucin da yake yi ya tunkari inda yake da gaggawa, doctor ya akai?? ya ake ciki?? zata lafiya kuwa??

Ya tambaya cikin tashin hankali.

Likitan ya dubi nurses din dake tare dashi yace " kuyi ku samo abin nan yanzu ".

To suka fada tare da wucewa.

Ya juyo ga ahmad yace " Karka shiga damuwa da yawa zata sami sauki bada jimawa ba insha Allah, mun shawo kan abin sai dai har yanzu bata farfado ba.

Idan mahaifinta ko mahaifiyarta sunzo ina son ganinsu a ofis."
Ya wuce da sauri.
Ahmad baiyi wata-wata ba ya fada dakin kai tsaye izuwa gabanta yabi ta kallo cikin sanyin jiki, ALLAH SARKI humaira zuciyarsa ta fada.
Ya danja da baya ya zauna a kujerar dake gefen gadon da take kwance har yanzu idonsa akanta yake.
Abinda ya fara fado masa arai shine: Tayaya za'ai iyayenta ko wani nata yasan halin da take ciki tunda bashi da zabi dole sai hakan ta faru.
Tuno da wayarta da yayi wacce ke rike a hannunsa yasa yayi saurin dagota kai tsaye ya shiga contacts dinta, abin mamaki ba wasu lambobi ne da yawa a ciki ba, ya tsa ya a dai dai lambar da aka sa MY MUM, ya danyi jim kamar me jin tsoron kiran bisa dole ya danna kira tare da karata a kunnensa.
Yayi shiru ya kasa magana har sai sanda wacce ta daga wayar tace " humaira Ify shiru har yanzu??
Ahmad dakyar yace " ba ita bace ni sunana Ahmad ina fatan kece mahaifiyarta??"
Ehh... nice.... mahaifiyarta Ify dai ko??
Ta tambaya da sauri.
Humaira ta yanke jiki ta fadi yanzu haka muna asibiti...."
Subhanallahi!!!! Ta fada cikin rudewa tare da cewa kuna wane asibitin ne??
Ahmad cikin sanyin murya yace " ALBARKA HOSPITAL dake nan cikin........."kafin yakai karshen maganar ta katse wayar.
Yabi wayar da kallo lokaci guda ya juya ga fuskar humaira yabi ledar ruwan da aka jona mata da kallo izuwa inda yake a rataye can sama, ya dafe kai, ko kadan baya son kallonta musamman idan ya tuno abinda ya faru kafin shigarta halin da take ciki.
mintuna talatin ya sake shafewa kafin mahaifiyarta da wata da baisan ko wacece ba suka zo, da tambayarshi suka fara.

Ahmad yace " muna cikin magana to sai ta mike lokaci guda kuma ta yanke jiki ta fadi. mahaifiyartata tace " to yanzu me likitan yace??"
Ahmad yace " cewa yayi idan wani yazo daga cikinku yana bukatar ganinsa.
Mahaifiyar tata ta dafe kai tace " humaira ban taba ganin mutum irinki ba, ace ke ba zaki taba manta baya ba? ba zaki taba daina tunanin abinda ya wuce ba? Wasu hawaye suka gangaro mata, wacce suka zo taren ta fara rarrashinta, Ahmad kuwa binsu kawai yake da kallo.
Ta juyo ga Ahmad tace " sai kayi kokari ka tafi tunda munzo kada dare yayi maka.
Ya gyada kai kawai ba tare daya motsa ba, ya dade kafin ya tashi ya mika musu wayar humairan kamar mara laka a jiki a haka ya fita daga dakin.
zuwansa motarsa keda wuya yayi arba da jakar humaira ya dago ta tare da jujjuyata a hannunsa yasan tabbas tana ji da kyakyawar jakar tata sbd kusan kowanne lokaci da ita yake ganinta.
Kamar ya fita yakai musu ita sai kuma ya fasa ya jawo kofar motar tasa ya kunnata yabar harabar asibitin.
Jikinsa a sanyaye yake tukin, jinsa yake kamar sabon mara lfy a haka ya iso gida, da sauri ya wuce izuwa ciki yadda yake so kuwa momi bata falon sai saudat kadai kwance tana danna wayarta.
Ta amsa sallamar tasa kanta nakan wayar tare da cewa yaya ka dawo??
Ehh... na dawo ya fada tare da wucewa da sauri kafin ta dago kai izuwa dakinsa, dai dai sanda ta tashi zaune tabishi da kallo a ranta tace " Wannan lfy?"
jim kadan ta dan daga kafada tare da komawa ta kwanta.
Yana shiga dakin nasa ya mayar da kofar ya rufe ya jingina a jikinta idonsa ya ciko da kwallah a hankali ya karasa ya jefa jakar tata

kan makeken gadon dake dakin, fadawar jakar keda wuya ta bude abinda ke cikinta ya fito wanda yayi saurin canja fuskar Ahmad.
Wani katon littafi ne me tsawo, fadi da yawan gaske.
Ya zauna a gefen gadon a hankali ya jawo littafin ya kare mai kallo a haka a hankali kuma ya bude bangon littafin idonsa yayi saurin kara zarowa sanda yaci karo da hoton humaira me matukar kyau da haiba a kasa an rubuta AISHA HUMAIRA ISMA'IL ya karewa hoton kallo sannan ya bude shafin gaba anan ma hoto ne amma ba nata ba, wani kyakyawan saurayi ne da shekarunsa basu haura Talatin da daya 31 ba, kyakyawa ne na gaske a kasan sunan nasa ansa UMAR FARUK ABUBAKAR, Ahmad ya dade yana kallon hoton nasa ya sake bude shafin gaba nan kuma hotuna ne nata da wancan faruk din a samansu ansa FARUK & HUMAIRA, tsakiyarsu kuma dan gaf fin dake tsakaninsu ansa ONE LOVE!! daga kasa kuma ansa LIFE TOGETHER DIE TOGETHER.
Littafin ya subuce daga hannun Ahmad sbd mamaki, dama halin da take ciki akan soyayya ne??
Waye kuma wannan faruk din??
Tambayoyin da suka fara zuwar masa kenan.
Ya sake cakumo littafin da sauri ya bude shafin gaba na tafkeken littafin yaci karo da abinda yasa shi saurin gyara zama CIKAKKEN LABARINA.
labarin humaira kenan?? ya tambayi kansa, yayi saurin gyara zamansa ya karasa karanta abinda aka rubuta a kasa, labarin farin ciki na gajeren lokaci daya jawo bakin ciki na har abada.
Labari me tsuma zuciya da sanya shauki.
Labari me tare da tarin Al'ajabi.
Ahmad bude shafin gaba ya fara karanta labarin humaira daya dade yana burin ya sani.
Cikakken SUNANA Aisha humaira, sunan mahaifina Alhaji Isma'il ishak daya daga cikin

hamshakai kuma fitattun yan kasuwa a africa. Haifaffiyar garin kano unguwar hausawa......kuma SABAHUL KHAIRI...
Shine yadace da masu karatu..
Se ku qara gyara xama dan sauraro da karanta labari me cike da AL-AJABI....
.
CIKAKKEN LABARINA. labarin humaira kenan?? ya tambayi kansa, yayi saurin gyara zamansa ya karasa karanta abinda aka rubuta a kasa, labarin farin ciki na gajeren lokaci daya jawo bakin ciki na har abada. Labari me tsuma zuciya da sanya shauki. Labari me tare da tarin Al'ajabi. Ahmad bude shafin gaba ya fara karanta labarin humaira daya dade yana burin yikakken SUNANA Aisha humaira, sunan mahaifina Alhaji Isma'il ishak daya daga cikin hamshakai kuma fitattun yan kasuwa a africa. Haifaffiyar garin kano unguwar hausawa......kuma Ya kasance sananne wanda sunansa ba boyayye bane sbd Allah yayi arziki na gaban kwatance, hakan yasa ya tara mutane masu yawa matuka kama daga ma'aikata, abokai da yan maula daban daban dake kaiwa dake nanike dashi a kowanne lokaci. Ni kadai ce wacce mahaifina ya mallaka a matsayin Y'A hakan yasa na taso cikin gata, so, kauna da kulawa. Tun daga yarintata ba abinda nake nema in rasa, komai nace ina so sai an mallaka min ban taba yin kukan rashin wani abu ba. a kowanne lokaci mahaifina na nuna min ba abinda bazan samu ba sai dai idan bana so, tun dai bana yarda har na yarda domin kwakwalwata ta gaza tunano min abinda zan nema dukiyar mahaifina ta gaza samar min shi. Saboda son da mahaifina keyi min yasa kowa ke nan-nan dani da nuna kulawarsa akaina don ya samu abinda yake so a wurinsa, duk kuwa wanda ya kuskura ya taba ni to kashinsa ya bushe a wurin mahaifina. Matsala daya dana tashi da ita itace na raina mutani da nayi musamman talakawa da marasa galihu, gashi ko kadan

bana son kula mutane bare na girmamasu sbd bana ganin kan kowa da gashi. ban damu na shiga harkar kowa ba kuma mafi yawa idan aka shiga tawa raine ke baci, hatta kawaye ban damu nayi ba sbd yadda nake jin nafi kowa. Ba wadanda nafi rainawa na taka yadda raina ke so irin yan aikin gidanmu kuma dole su kalleni don suna tabani sun san hukuncinsu kora ne don haka dole suka kyaleni nake cin karena ba babbaka, mutum dake da karfin taka min birki a wasu lokutan itace mahaifiyata da nake kira da MUM.

.

Wani lokacin idan na dauko rashin mutuncin daya wuce hankali takan kwabe ni wadda ita kadai ke yin hakan domin mahaifina komai nayi dai dai ne a wurinsa.

.

********* ************ *********

.

Tun ina da shekaru hudu aka saka ni a nursery ta musamman ba kamar saura ba, me tsadan gaske ce da kudin da ake biya a shekara daya kawai ya isa a dauki nauyin karatun yayan talakawa guda uku tun daga primary har zuwa jami'a. Direrba aka tanada don kaini kuma ya daukoni, idan ya kaini baya tafiya har sai an tashi ya dawo dani. Shekaru biyu kacal nayi aka matsar dani izuwa hamshakiyar makarantar da duk wani dan me akwai ke burin ganinsa a cikinta, wadda tun daga sunanta kasan tafi karfin talaka koma uban talaka, makarantar nada kyan yanayin data burgeni har yakai ban taba korafi da ita ba. Ina daya daga cikin dalibai abin alfahari a makarantar sbd kwakwalwata ta saurin gane abu wanda hakan ke kara min girman kai matuka. Duk da cewa makarantar kowa naji da kansa domin ba dan talaka a cikinta kowa ka gani daga gidan arziki yake, amma fa nawa girman kan yafi na kowa domin ko kawa daya ban yi ba sbd a ganina duk babu me aji dai dai dani. Sai dana shafe shekaru goma sha biyu

anan primary & secondary, da shekaruna 18 na gama ta.

.

A dai- dai wannan lokacinne kuma kari kan da ZUNZURUTUN KYAU ya kara bayyana, Wohoho!!!!!!!!!! Kai idan ka ganni sai ka rantse da Allah ni balarabiya ce domin kadan zubi na bana hausawa bane, kamar yadda ake fada kuma nake gasgatawa a duk sanda na dubi kaina babu kamata a wannan zamanin indai fagen kyau ne. Nasha jawo accident idan ana tafiya dani a mota ban daga glass ba, nasha jawowa mutane karo da juna idan ina tafiya, duk wadda ke ji da kanta idan ta ganni sai ta fashe da kuka don taga karshen kyau, wasu fashewa suke da kuka suna cewa ina ma su sami 1/10 kyawu na. Kwalliya ma bata wani dameni ba sbd a cewata idan kyau bai cika bane ake neman kwalliya ta karasa cikashi amma idan kyau ya cika babu bukatar hakan. Mafi yawa harkar sharwoliya bata dameni ba koda a shigata nakanyi kokari na rufe jikina, mafi yawa kayan da nafi sawa ba wadanda basu kamata bane sbd ni ako yaushe na yarda na tsare mutuncina kuma a ko'ina. Bayan na kammala secondary a nigeria mahaifina ya nema min admission amma fa a oxford university dake kasar england, nayi murna sosai sbd ina da buri na bar kasata izuwa wata musamman kasashen turai. Da yake harka ce ta kudi nan da nan komai ya kammala kuma aka saka ranar tafiyata domin fara degree na farko a fannin kimiyar tattalin arziki wato (economics) da kuma lissafi. Ana gobe zan tafi ne bayan komai ya gama shiryuwa zaune nake nasa tafkekiyar televission din dake manne a jikin bango nesa kadan dani a cikin katafaren falon alfarma na gidanmu, cikin kwanciyar hankali nake kallon ba wani abu dake damuna. kaso 99% na hankali ya tafi ga kallon film din na DHOOM yadda jarumin film din ke raina hankalin yan sanda da dabaru daban daban, wucewar da

daya daga cikin yan aikin falon tayi ta gabana yasa banga karashen abinda ya faru ba abinda ya tunzira ni kenan wulakancina ya motsa na kira sunanta da karfi.
.
HANNE!! Ta juyo da sauri tana kyarma, nace " Zo nan" Ta fara matsowa a hankali a hankali na daka mata tsawa nace " gidan uwar wa zaki je??" Tace " uhm... haji..ya ce ta kira...ni. ". Nace harareta nace " kuma don ubanki shine ta gabana zaki wuce ko? Duk nan ba hanya bace??" Tayi shiru kawai tana makyarkyata bata ankara ba na zabga mata mari hade da fadin " ba tambayarki nake ba??". Karfin marin sai daya sa ta fadi kasa lokaci guda ta zarce da kuka." Ahmad ya kauda littafin daga karantawar da yake yace " Lallai wannan wulakanci har na siyarwa kina dashi ya gyara kwanciyarsa tare da mayar da idonsa ya dora da karantawa.......
.
Karar data kwalla ne ya jawo hankalin mum ta fito da sauri tana tambayar lafiya kuwa?? Ta tsaya kawai tasamu a gaba tana kallo hade da hararata cikin takaici.......
AL'AJABI part 6
NA ABUBAKAR A. MUHAMMAD
wth--------->
Aßu Fer'ezerh
MUM ta dade tana kallona cikin takaici jim kadan tace " Me tayi miki kika mareta??"
Na koma kan kujera na zauna nace " zuwa... tayi ta giftani ina kallo ta kare min ban gani ba kuma tambayarta tayi min shiru."
ta kada kai tace " lallai humaira rashin mutuncin naki yakai, kawai daga na kirata ta gifta ta gabanki shine abin duka??"
Na zunburo baki nace mum " kare min fa tayi kuma......."
Ta katse ni da cewa " ke dalla can rufa mana baki kice kawai wulakancinki ya motsa to kin daketa kinji dadi, idan kinfi karfinta ai akwai Allah."
Ta nufi inda hanne ke zaune har yanzu bata tashi

ba sai kuka da take yi.
Na dan kara bata rai tare da gyara zama nace " ni mum wlh bakya yimin adalci a komai ba zaki taba goyon bayana ba kullum nice me laifi a wurinki akan wadannan banzayen."
Nakai karshen maganar da kauda kai.
Mum tace " anki a goya miki bayan wace gsky gareki?? Ke ko kunya baki ji ba don Allah?? ki rasa wacce zaki zage kwanjinki akanta sai yar aikin gdnku wadanda yakamata ace kin jasu a jikinki ki nuna musu kauna."
Na kalli hanne na zabga mata harara nace " wadannan shashashan matsiyatan zanja a jikina?? Allah ya kiyaye.
Mum tace " to tunda ba zaki kyalesu susha iska ba ba ruwanki dasu basu shiga rayuwarki ba kada ki kara shiga tasu idan kuma kika ku wlh zan basu dama idan kika dakesu su rama suyi miki dan banzan duka ai ba karfinsu kika fi ba. Taja hannunta suka wuce, nabi mum da kallon mamakin jin abinda ita kanta tasan bazai yiwu ba, nace " Su dakeni fa kika ce?? "
Ta juyo da sauri tace " Eh don ubanki ".
Nabita da kallo ganin abin ya dau zafi da yawa ta juya suka bar falon da nake a zaune.
Na gyara zama na hade rai nayi kicin-kicin kamar na fashe da kuka, wai ni ake zagi akan wannan banzar yar aikin? lallai zamanta yazo karshe a gidan nan bari dady ya dawo.
BAYAN AWA DAYA naji motsin dawowar dadyna na kakalo sabon fushi da takaici, dady yana shigowa yayi ido hudu dani cikin fushi, yayi saurin ajiye jakarsa tare da tunkaro inda nake zaune " my daughter ( daya daga cikin sunayen da yake kirana dasu ) menene ya faru haka? waye ya taba min ke?"
Nayi shiru na kara hade rai kawai na juyar da kaina.
Dady ya zauna gaf dani cikin kasa-kasa da murya yace " fada min mana waye ya taba ki? uhummm?"
Cikin shagwaba na mirgina kai nace " ba mum bace......."

Me kuma tayi miki??
Ya tambaya da sauri.
nace " wai..... zata sa yan aiki su rinka dukana "
dady har wani dan babban motsi yayi tare da mai-maita abinda na fada " su dakeki??".
na gyada kai.
Ya juya da sauri ya fara kwallawa mum kira.
Hajiya!!!!! Hajiya!!!!!
Da saurinta ta fito izuwa falon da faddady yace " Me yasa kika batawa humaira rai, wai ke hajiya me yasa kike haka ne don Allah.... to to yanzu me kike nufi yar aiki tafi yar da kika haifa da cikinki kenan??"
Mum ta tabe baki tace " au wai da akan wannan ne kake kwala min kira haka sai kace wani tashin hankali??"
Au kina nufin shi wannan ba komai bane kenan?? kinga hajiya ran kowa zai baci a gidan nan fa.
Mum tace " rainin nata ne yayi yawa nace zansa a dai daita mata zama.
Na tsandara ihu nace kaji ko dady??
Dady ya kara rudewa ya fara zabga bala'i ta inda ya shiga batanan yake shiga ba.
Zuwa can nace " dady kawai a kori yan aikin nan dukansu ".
dady ya juyo yace " kwantar da hankalinki, abinda za'ai kenan suna ina ne??"
Mum tace " Wai suwa za'a kora?? bazai yiwu ba sbd duk cikinku ba wadda kuka dauka kuma baku kuke biyansu ba nice don haka babu me korar minsu ina jin dadin aiki dasu......
Munji tafi kici gaba da harkokinki kada ranmu ya baci duka, Allah ya baka hakuri.
Ta juya ta nufi sashinta, dady ya juyo gareni ya fara rarrashina ni kuwa sai wani kara hade rai nake.
Kinga manta dasu kinji humaira na, ba wanda ya isa ya taba ki duk wanda ya kara bata miki rai wlh tamuce ni dashi.
Kada ki manta fa gobe iwar haka kina kasar birtaniya kin bar musu kucakar kasar tasu zaki fara rayuwa cikin turawa ba wanda zai takura miki inda iskar da zaki shaka ma ba irin wannan

bace.
Jin hakan da nayi yasa nadan saki raina kadan, yace " to danyi murmushi mana "
Na saki rai sosai yace " Yauwa ko ke fa! gobe kiyi kokari ki tashi da wuri sbd jirginki na safe ne an gama duk wasu shirye-shirye kina zuwa direct zaku daga shuuuuu!!! sai london."
yakai maganar da murmushi.
Na dan tabe baki cikin shagwaba nace " dady nifa dakai zamu tafi idan muka je sai ka dawo."
Ya dubeni yace " to ke banda abinki ina naga lokacin binki har london kuma na dawo? kedai karki damu jirgin na musamman ne zaki samu duk abinda kike bukata kuma za'a kula daku sosai musamman ma ke yar lele.
Nayi murmushi kawai.
Daddy ya mike ya dau jakarsa bari na shiga ciki ko?
"To dady" Na fada idona na kasa ya wuce.
Na daga kaina na dubi katafaren agogon dake manne a jikin bango karfe 6:15pm sallar magaribar ma ai da saura na mayar da kaina ga t.v din naci gaba da kallo.
$$$$$$$$$$$$
in Alhaji Ify irin wanWashe gari misalin karfe 8:00am na safe zaune muke mu uku, mum da dady na zaune a kujeru daf da juna yayinda nake zaune a kujerar dake fuskantarsu.
faffadan tebirine a gabanmu kayan abinci kala-kala jere bisa kansa wadanda suka dace da karin safe, babu wanda ke magana a cikinmu.
Humaira!!!!!!!!!!!!
dady ya kira sunana, na dago a hankali na dubeshi.
yace " misalin 11:30 na safen nan zaku tashi, abinda nake so dake shine kibi a hankali kuma ki kula sosai sbd kasar da zaki je ba taki bace ba wadda kike ciki bace kuma ba wadda kika saba da ita bace, kiyi abinda yakai ki kawai shine karatu ki samo abinda zanyi alfahari dashi sbd ina da comfidence 100% akanki kuma ba zaki bani ba.
Insha-Allahu dady. Na fada tare da mayar da

kaina ga kofin tea dake hannuna.
Daddy ya mike yace " bari inje na shirya na fita ina da meeting karfe tara hajiya ina takardun nan dana baki ajiyansu jiya??
Ta dago kai a karon farko tace " Suna nan cikin lokar sama." Ok " ya fada tare da dubana yace " yar lele na Allah ya kiyaye hanya, da zarar kun sauka zanyo miki waya."
To dady na fada ya juya nudi dakinsa.
Na mike na koma kan kujerar dake gaf da mum nace " Momina banji kince komai ba."
To me zance???
Ta fada kanta na duban abinda take ci.
Nace yakamata kice wani abu saboda kinga tafiya zanyi ta shekaru da yawa kodai bakin cikin rabuwa dani kike yi da yawa haka har ya hana ki magana??"
A'A ta fada tare da cewa " nifa haushinki kawai nake ji "
Na bita da kallo lokaci guda nayi yar gajeriyar dariya nace " da gaske??"
ta gyada kai kawai.
Na kwantar da kaina a jikinta nace " sorry my mum ai nasan da wasa kike ba zaki taba jin haushi na ba, uhmm! mum pls sarkar nan don Allah ki bani zanyi amfani da ita acan.
Ta girgiza kai tace " kefa kika nuna halin ko in kula da ita sai yanzu zaki ce kina so??"
Mum dama can ina sonta wlh zan kula da ita, Zaki bani??
nakai karshen maganar da kwantar da murya.
Mum ta dubeni kadan ta kauda kai tace " Zan baki ".
Na saki fuska hade da alamar jinjina nace " Thank you MUM bari naje na fara shiri. "
Na nufi dakina.
Misalin karfe goma 10:00am mufida tazo kawowa momi sako ta iske ina gaf da gama shirina ta tayani muka karasa na tilasta mata ta tsaya don yimin rakiya izuwa airport.
MUFIDA y'a ce a wurin haj. jameela kawar mum kuma aminiyarta, mufida ce kadai zan iya cewa kawata a duniya don da ita kawai na yarda muyi

kawance sbd ta wasu bangarorin halinmu yazo daya duk da muna da banbanci da ita sosai a wasu bangarorin.
Misalin karfe 10:15am Nayi sallama da momi da sauran wadanda zan iya sallama dasu sauran yan aikin gidanmu kuwa da rashin mutunci muka rabu don ban hakura ba sai da nayi final.
A jibgegiyar mota kirar PRADO muka fito, mufida na gefena sai kuma mutum biyu har direba dake gaba.
Mukanyi hira jefi-jefi da mufida, kaina sai wani kumbura yake waini zani kasar turai.
Cikin kankanin lokaci muka isa AMINU KANO international airport, tunda naga jirgin dazai daga damu na yarda bana yara bane saboda haduwarsa, ya isa a nunashi a ko'ina.
Ban dauki lokaci ba aka gama tantanceni na juyo na karbi jakunkuna na mukai sallama da mufida...
****************************
Shigata jirgin ya tabbatar min da abinda dadyna ya fada, tsaruwarsa daga ciki yafi yadda nake ganinsa daga waje domin ya wuce duk yadda nake tsammani.
kai tsaye sit dina na wuce na zauna duk da cewa yaune karon farko dana shiga jirgi irin wannan amma ban yarda na nuna hakan ba don kada wadanda ke cikin jirgin su raina ni.
Abinda na lura dashi shine kowa naji da kansa a cikin jirgin sbd daga manyan attajirai masu tafiya kasuwanci sai yayan attajirai masu zuwa karatu irina, babu ma zaton samun dan talaka a ciki bare a samu din. Kamar yadda aka shirya 11:00am dai dai jirgin ya daga kai tsaye izuwa birnin london tafiya mafi tsawo dana fara yi a rayuwata, jami'an cikin jirgin kuwa sai nan nan ake damu duk abinda muka bukata ba bata lkc ake bamu.
Awanni nata shudewa 2n ina sha'awar tafiyar har sai dana gaji amma bamu iso ba, duk na kosa sbd wannan ne karon farko dana taba yin tafiya irin wannan daga karshe madai wani nannauyan barci ne ya kwashe ni ban farka ba sai AIRPORT na birnin londôn, A hankali daya bayan daya

muka sakko daga cikin jirgin.
wowwww!!! Nan fa naga abin mamaki domin ba birnin ba airport din kadai abin kallo ne ban taba tsammanin akwai wuri me kyau da kawatuwa irin wannan lallai duk yadda ake bada lbrn birnin nan ya wuce nan, duk yadda nakai da ji da kai sai dana zama kamar wata yar kauye a wurin.
saukowarmu keda wuya jami'an filin jirgin suka yo kanmu nan fa aka shiga secreening kala-kala harda wanda ban taba ji ba ko a lbr, bayan na cika duk wani sharadine aka bani damar ficewa daga airport din, ban jima ba kuwa wata jibgegiyar mota me matukar fadi da tsawo ta iso like take da banner din OXFORD UNIVERSITY bamu dauki tsawon lokaci ba ta debemu tare da mutane daban-daban da muka zo daga wurare da kasashe maban-banta, Anan ne fa naji kwalta tamkar ita ta shimfida kanta, duk inda motar tabi titine luwai-luwai ba gargada bare rami.
Shuuuuuuu!!!!! A haka motar ke tafiya tamkar jirgin sama ban-bancin kawai ita wannan a kasa take tafiya ba'a sama ba.
Gefe guda tsarin gine-ginen birnin wanda keda matukar tsayi tamkar zasu tabo can kololuwar sama sun kawatar dani matuka.
gashi kowa irin rayuwar da nafi so yake yi ta ba ruwan kowa da wani, kowa ka gani harkar gabansa yakeyi. jim kadan muka iso katafariyar jami'ar daya daga cikin mafi girma, daukaka da suna a duniya, bayan komai ya kammalu kuma kai tsaye aka yimin jagora izuwa masaukina.
Ni kadai ce a sashin nawa wanda ya kunshi duk abubuwan da nake bukata.
************************* Nan fa na shiga karatu gadan-gadan kasancewarsa wajene da ko baka so sai kayi karatu, da farko na dauka a nigeria ne naci gaba da jiji dakai da takama sai naga ina!! domin a banza wajene da kowa keji da duk abinda nake ji dashi shima. Dole tasa na sakko na fara maraba da kowa nan da nan kuwa na tara kawaye masu yawan gaske tamkar bani ba, na saki jiki da mutane sosai. Da yake ba karatu ne irinna na nigeria ba cikin shekaru biyu kacal

na kammala degree na na farko a hakan ma don
mun sami dan tsaiko ina daya daga cikin
wadanda suka sami sakamako me kyan gaske
hakan yasa makarantar ta bani damar yin
masters degree kyauta kasancewar ina jin dadin
zaman yasa na amince na zarce cikin ba tare da
jinkiri ba. shekara daya kuma na kammala
masters, degree biyu cikin shekaru uku kacal,
wannan shine tarihin kara2na da yadda na samu
masters degree a kasar birtaniya.
“hmmm..... Lallai gskyr Bahaushe da yace ‘Talaka
bawan Allah‘ domin talakan nigeria ne zai kwashe
shekaru hudu yana neman diplomer bai samu ba“
Ahmad ya fada sanda ya kauda kansa daga kan
littafin lkc guda ya mayar da kansa ya dora.
kammaluwar komai tasa na tattaro inawa-inawa
nayo nigeria, ranar laraba misalin 12:00pm
jirginmu yayo nigeria.
dirarmu keda wuya dady ya iso tare da wasu
daga cikin yaransa aka daukeni direct mukai gida,
nan fa girman kai, takama, gadara da raina
mutane ya dawo sabo fil. Na fara jin nifa yanzu
nafi kowa kuma samun kamar ni sai an tona kai
zaiyi wuya ma a samu mace kamar ni da tattara
abubuwan da nake dasu.....
Hmmm'un yanxu akapara shirin..!
BARKAN KU DA ASUBAH..!
Bayan kwanaki uku da dawowata ina kwance
bisa doguwar kujera hannuna na rike da wani
novel daya daga cikin abokan hirata a london
me suna HAPPINESS DAY na prof. christiana
wolein dan kasar holland, kyakykyawar fuskata
nakan littafin wanda fararen idanuna ke kallo,
hankalina, tunanina da duk wani nazarina ya
tafi ga karanta daddadan Ibrn da nake yi
wanda nake matukar son karasashi ko don naji
yadda karashen Ibrn zai kasance.
Magribar da nake ganin ta doso yasa na kara
kaimi, Momi ta fito daga sashinta rike da wani
dan madai-daicin kaskon turare wanda wani
daddadan kamshi ke tashi ta hanyar farin
hayakin dake fita daga kaskon, ta fara zagaye
faffadan falon domin kanshin ya isa ko‘ina

kafin ta dawo ta ajiye shi a tsakiyar falon.
A dai-dai Ikcnne dady na ya dawo, cikin fara'a yayi sallama kasancewar ya ganni a falon, ya karasa ya aje jakarsa tare da zama. Kamar hadin baki nida momi muka amsa sallamar, na dago daga kwanciyar da nayi tare da aje novel din a gefena nace "Wellcome back my dady".
Yauwa yar lele na da fatan dai komai normal ko? na gyada kai kawai, momi dake gefe ta bimu da kallo tare da jinjina kai tace "uhm.. gsky ina ganin kabilanci a gidannan, wato Alhaji yarka kawai ka sani ni ba mu2m bace??" Daddy ya kyalkyale da dariya yace "kinji ki hajiya da wani zance gani kikai na tashi daga nan bance miki komai ba??" Da sauri tace "zaka iya don ba karamin aikinka bane kace bama ka ganni ba 2nda ka shigo sai da nayi magana." Dady ya sake yin dariya yace " A haba sai kace wani makaho? kawai dai........" Y'arka ce a ranka!! momi ta karasa masa zancen.
ya gyada kai yace "anji muje a hakan". Momi tace "gashi kuma duk daran dadewa sai ka shigo falon nan ka tarar batanan koka manta macece dole ka aurar da ita??" Dady yayi murmushi yace "kinga hajiya duk takaicinki kyayi ki gama ai ba akuya bace ita bare kice zan kaita kasuwa na siyar mun rabu kenan har abada."
Duk muka fashe da dariya, dady ya kwantar da kansa jikin kujerar yace " yauwa ni na tuna ma, humaira!!
Na dago kaina a nitse domin nasan indai dady ya kira sunana kai tsaye to maganar da yake son yimin me muhimmanci ce.
Yace "kasancewar kinyi kara2 me tsada a wuri me tsada kuma akan abu me tsadan gaske izuwa yanzu na sami request daga wurare daban-daban akan anaso ayi aiki dake, daga ciki akwai central ban.k da me gwamnan bankin da kansa ya rubuto min takarda akan cewa suna bukatar karin kwararru da suke da sani akan tattalin arziki, akwai FIRST BANK,

GTI BANK, DIAMOND BANK da sauransu.
Ma‘aikatar kudi ta tarayya ma na bukatar kiyi aiki dasu, sannan jami‘o‘i kamar B.U.K, A.B.U da sauransu na bukatar kiyi musu aiki a matsayin lecturer, ke harda wasu hukumomi daga kasashen waje sai kin zaba kin darje.
A maimakon nayi farin ciki sai na hade rai, dady ya dubeni tare da gyara zama yace “Ah ya naga kin bata rai?? lafiya??“
Na dan kumburo baki nace “dady nifa bazanyi wani aiki a duk wuraren nan ba.“
dady yace “sai a ina?? ko a bankin duniya kike so kiyi aiki??“
Na girgiza kai nace “ A‘A ni bazanyi a ko‘ina ba.“
Kafin yace wani abu momi tace “ba zakiyi ba kina nufin duk kara2n da kikai ya tashi a banza kenan??“
Dady ya dubeta yace “haba hajiya kibita a hankali mana, ya juyo gareni yace “Yar lelena me yasa bakison kiyi aiki??“
Nace dady nifa banyi kara2 don na wahalar da kaina ba, nawa ne duka albashin da za‘a biyani? duka fa bai kai kudin da gyaran gashi na keci ba.
Yayan talakawa da matsiyata sune keyin kara2 don su sami aiki amma ba irina ba.“
Daddy ya kyalkyale da dariya kamar zai tuntsiro daga kan kujerar yace “gskyrki fa y‘ata.“
Momi tace “ Au wai kaima ka biye mata a hakan??“
Daddy yace “To karya tayi??, ya juyo gareni yace “ yanzu ke me kike so ayi??“.
Na tabe baki kamar ba zance komabi ba daga bisani nace “ daddy nifa a duniya ba abinda ban iya ba irin kwamfuta don haka ina son na samu certificate akanta.
Cikin sauri daddy yace “Tooo!!! a germany ko japan ko america zabi daya......
Na tabe baki nace “NO daddy duk basai ankai ga haka ba, anan kano nake so nayi.“
Daddy yabini da kallo yace “kina nufin a

makarantar matsiyata??“ Dariya ta kwace min na girgiza kai nace “ a‘a akwai wata reshen AL-KHRAMY ta kasar saudiya da suka bude anan kano next week za‘a fara lecture, MUFIDA ma can zata fara zuwa kaga na sami abokiyar tafiya.“
Daddy ya gyara zamansa yace “kwarai naji Ibrnta, to karki damu my daughter a ckn satin nan za‘a shirya miki komai next week dake za‘a budeta.“ Nayi murmushi nace “Thank you my dad“.
Daddy ya mike “bari in karasa ciki, ya juyo ga momi yace “a ina kika saka min jakar nan ta jiya??“ Har yanzu takaicine akan fuskarta tace “ tana nan cikin lokar dakinka“. daddy ya sabi jakarsa ya wuce. Ni kuwa wani farin ciki ya lullubeni, gsky daddy na sona ni kaina nasan haka.
Hararar da momi keyi min ce tasa ban takalo wata hira da ita ba na jawo novel dina tare da kwanciya bisa luntsimemiyar kujerar da nake kai na cgb da kara2n da nakeyi a baya.
******** ******* ******* ********
Sati daya dai-dai da faruwar haka na fara zuwa lecture a katafariyar makarantar AL-KHRAMY computer training school, 2n daga sanda na hangi makarantar a shigata ta farko naji a raina tayi min sbd tsarinta. fasalin gininta kawai abin kallo ne banda kuma zubin cikinta.
Tana da ma2kar fadi da girma da kuma wadatar dakunan kara2, akwai bangaren da aka ware musamman don hutawa a lkcn da ba‘a lacca wanda ya kunshi kujeru a jere daf da wasu kyawawan bishiyu da kuma filawowi dalilin da yasa iskar dake kadawa a wajen ta zama me kamshi, wajen dai ya dace da hutawa ga wanda ya debo gajiyar kara2.
Gefe guda akwai daki na musamman da aka ware aka cikashi da littattafai kala-kala da suka shafi darasin computer da mutum zai iya zuwa ya bincika wanda yake so, nesa kadan kuma akwai wurin cin abinci da aka ware

musamman ga masu bukata.
Da yake makarantar mallakar larabawa ce an ware bangaren maza daban na mata daban. Ga yadda ake kaffa da dalibai ake maidasu y‘an gata.
kamar yadda aka saba ranar juma‘a 12:00pm mun tashi zaune nake bisa wani dan dandamali ina jiran mufida ta fito mu tafi kaina na kasa na kurawa laptop din dake bisa cinyoyina ido ina tayi, sallamar da naji anyi ce tasani dakatawa kamar na dago kai na dubi wanda yayi sallamar sbd muryar tasa ta ratsani sosai amma sai girman kan ya motsa na cgb da abinda nakeyi ko sallamar ban amsa ba.
Kyakykyawan saurayin bai gajiya ba yace “ pls na gaji da tsayuwa in zauna??“
Na cilla idona tare dago fuskata nace “ka zauna mana idan ka gadama“.
Mai makon ya bata rai sai yayi murmushi yace “godiya nake.“
Ya zauna bisa dandamalin nesa kadan dani, kaina na kasa amma zuciyata na sake-sake, ji nake kamar na dago kalli mu2min daya fara birgeni karo na farko a rayuwata.
Jim kadan mufida ta fito ai kuwa tana kyalla ido taga wannan saurayin dake kusa dani sai ta bude baki tare da fadin “ Ah leader manyan gari kaine anan haka??“
Yayi murmushin daya kara masa kyau yace “nine wlh kinga su nazir nake jira basu fito ba dama tare kuke da wannan??“
yayi nuni dani.
Eh tare muke da ita wlh ni take jira......
Na rufe laptop dina tare da diban littattafaina dake ajiye a gefena na doka tsaki na wuce nabarsu anan.“
mufida tabini da kallo kawai ta juya tare da yin murmushi tace “sai gobe ko??“
Ya gyada kai kawai dai-dai lokacinne abokansa su uku suka karaso wanda ya riga kowa karasowar yace “kai wai ya akai harka 2nkari wccn yarinyar ta barka ka zauna kusa

da ita??“
Ya bishi da kallo yace “kasanta ne??“
Kwarai kuwa shugaban y‘an girman kai, takama da gadara ta duniya kenan.“
duk sukai dariya, saurayin ya shafi gashin kansa yace “kai! nazir yarinyar fa ba karya wlh ta hadu“, wanda aka kira da nazir din yace “ ana fada maka matsalarta kana cewa ta hadu??“
ya harareshi yace “ mace idan batai takama da gadara ba waye zaiyi?? girman kan ne kawai matsala.... ya sake bin inda muka bari a mota da kallo.“
Ni kuwa 2nda muka tafi mufida nata bani Ibrn saurayin wai mu2min kirki ne kaza-kaza nidai ban kulata ba, don kasa gane me take nufi da hakan....
Ammafah....koda baxance komaiba..senaga iya gudun grman kannata....
Yanxu ne aslin komai ze fara..sekucigaba dabina.. amma fa bada gudu ba
Isata gida keda wuya na ketawa ma‘aikatan gdnmu rashin mu2ncin dana saba harma sai dana mari me baiwa fulawowi ruwa sbd yayi sakacin watsa min ruwa duk kuwa da cewa ba yana sane bane, kai tsaye dakina na wuce nayi wanka naci abinci na jawo laptop dina hau aikin dana saba.
Bayan kwanaki biyu da haduwa da saurayinnan da ko sunansa ban sani ba ina zaune a bakin harabar makarantar tamu a wannan karon wayata ce kawai a hannuna sakamakôn laptop dina tana hannun mufida, zuwa da wurin da nayi ne yasa a gabana dai-daikun dalibai ke isowa suna wucewa ba ruwana dasu sai dai su wuce.
wasu lktn zakaga daliban na zuwa ne a group-group kamar yadda al‘adar rayuwar makaranta take.
Ana cikin haka ne group din da suka fi kowanne shahara a makarantar suka zo wucewa ai kuwa caraf idon saurayinnan a kaina ya dakata tare da duban na kusa dashi

yace “nazir“.
Wanda aka kira da sunan nazir din yace “na‘am leader.“
wuce min da jakar nan na hango mu2niyar, nazir din ya amshi jakar ya kallo inda nake tare da cewa “wlh leader kabi a hankali yarinyar nan big class ce zaka sha mari fa inkai wasa.“
ya rike kugu tare da cewa “Ta mareni?? haba dallah sai kace a zamanin jahiliyya?? kudai ku tsaya kusha kallo.
Ya juyo ya doso inda nake, dirar daddadar muryarsa kawai naji a kunnena da fadin “Amincin Allah ya tbbta a gareki ma‘abociyar son kadaici da hutawa“.
Har ga Allah wani sanyi naji a raina amma da yake ni din ce kawai sai kauda kai kamar bansan me yace ba.
ya sake yin murmushi yace “kauda kanki Ify tauraruwa me haske“, na sake hade rai na kalli kasa.
woww!! gsky ke daban ce ban taba ganin wanda fushi keyiwa kyau ba sai ke.
Ya fada yana kallona. Na cije lebena na dubeshi zanyi magana yayi saurin cewa “ina ma kiyi magana a ckn fushi daba karamin kwarjini zaki kara ba.“
Na dan rufe idona a raina nace “BALA‘I“ na kara hade rai nace “kaga nifa ba shashasha bace da za‘a zo har inda nake a cikani da suru2 idan ina son zama a wuri me hayaniya mezai kawoni nan?
murmushinsa wanda adon fuskarsa ne ya karu yace “gani nayi zaman kadaici bashi da dadi shine nazo na debe miki kewa gashi kuma nayi nasara 2nda a baya bakinki a rufe yake yanzu kuma gashi yana motsi, na girgiza kai nace “to bana so idan wurin ne yayi maka zan iya tashi nabar maka“.
Ya mike tare da cewa “ kinfi karfin kina waje ace wani ya tasheki amma ki sani babu wata halitta dake iya rayuwa ita kadai dole tana bukatar mataimaki Allah ne kawai yake guda

daya baya bukatar abokin tarayya amma bamu
y'an adam masu rauni ba, yaja da baya tare
da dago min hannu yace "sai anjima".
Na bishi da kallo ba karya fa gayen ya hadu
wlh, tun daga zubinsa har ya zuwa kalamansa
da halayensa ababan birgewa ne.
Ban jima a zaune ba na tashi na shiga class
ko break ban fito ba sai da aka tashi, abinda
ya kara bata min rai sai dana shafe min2na 15
da tashi direba na bai iso ba bare mu tafi na
zauna bisa dandamalin dana saba zama na
zaro wayata na kira direban yana dagawa na
balbaleshi da fada duk da hakurin da yake bani
sai da nayi na gaji sannan na kashe wayar
hade da doka tsaki, Allah ya wuci zuciyarki
yake tauraruwa me kyalkyali, na dago kaina
muka hada ido da saurayinnan na bata rai
naja tsaki na kauda kai.
Yace "ina bbr aminiyar taki ne na ganki ke
kadai??"
sakanni talatin na dauka sannan nace " Ta tafi
koyo sallama "
Ya saki murmushi yace "sorry i took the
correction"
Amma me yasa duk ranar da ake kwallawa
baki nemi inuwa kin zauna ba kika zabi zama
a ckn rana??"
Cikin fusata nace "ina ruwanka? wai kai
wanne irin mu2m ne?"
Yace "bakar fata, musulmi kuma bahaushe,
bana fatan kice na takura miki don haka kinga
tafiyata, sai anjima."
MAYE!!!!!! na fada a raina, dai-dai Ikcnne
direbana ya karaso mufida ma ta fito kai tsaye
muka nufo gida, inata zabgawa direban ruwan
bala'i ta inda na shiga ba tanan nake fita ba.
******* Kwanaki uku da faruwar haka misalin
11:30am mun fito break da yake ban karya ba
naja mufida muka shiga restaurant aka kawo
mana abinci muka fara ci, bamu dauki tsawon
Ikc ba muka gama.
Na kira dan matashin bakin saurayin daya
kawo mana abincin nace "yauwa nawa ne

kudinku??“ yayi yar gajeriyar dariya yace “No ai basai kun biya ba“.
Na zabga masa harara nace “kai nifa bana wasa da yaro nawa ne kudinku aka ce??“ nakai karshen maganar cikin tsawa.
ya girgiza kai yace “An riga an biya muku fa“, na bishi da kallo nace “kai kada ka raina min hankali kaga nayi kama da matsiyaciyar da za‘a siya wa abinci?? To ai ni ko gaba daya restaurant din naku nagadama ina iya siya bare abincin mu2m biyu kada ka batamin rai ka batawa kanka, nawa ne kudinku??“
fuskar saurayin ta canja yace “haramun ne a aikina na karbi kudin mtm biyu akan abu daya amma idan kina musu ga wanda ya biya muku can, nabi hannunsa izuwa inda yayi min nuni caraf idanuna suka dira akan saurayinnan me lakabin leader na dauke kai tare da runtse idanuna ckn takaici, shit!!! wai wannan wane irin mtm ne?? Na tambayi kaina naja jakata dake ajiye akan tebirin dake gabana na doshi inda yake. Ko sanin nazo inda yake baiyi ba na tsaya a kansa nace “mallam abin naka kuma yana neman yayi yawa fa, daga ina dan saurararka kuma sai raini ya shiga??
cikin rashin fahimta ya ajiye kofin juice dake hannunsa ya dago kai yace “ raini kuma?? me ya faru??“ Na dan harareshi nace “idan ba haka ba meye na biya min kudin abu mafi sauki da kowa ke iya siya irin abinci??“
Fuskarsa tayi saurin canjawa zuwa murmushi yace “ wlh na zaci wani gingimemen laifi na aikatawa sarauniyar matan wannan karnin, ashe ma ba wani abu bane “ Na bishi da kallo nace “ba wani abu ba?? kayi min wulakanci irin wannan kace ba komai bane??“, ya juyar da p-cap din dake kansa izuwa baya yace “Ni banyi miki wulakanci ba a wajena kyautatawa nayi miki sbd kin cncnci fin haka a wurina bawai nayi hakan bane don kankantar dake domin kin wuce haka, kuma ni a wurina kyauta ai itace mafi girman karramawa!!
Ni kuma a wurina itace mafi girman

kankantarwa, nawa ka basu na biyaka??
Na fada dai-dai sanda na zaro wata yar karamar jaka daga bbr jakata.
Ya dago da sauri tare da bina da wani irin kallo tamkar bai fahimci abinda na fada ba yayi saurin girgiza kai yace “baki yi kama da wadda zata maida hannun kyauta baya ba sbd nasan kinsan hakan bai dace ba, abinda nake so ki gane shine don an baki abu kin amsa ba yana nufin baki fi karfin abin bane.“
Na tabe baki nace “well!! naji 2nda kai kagadama kaga zaka iya amma ka sani idan wai kayimin haka ne don naji dadi to banji ba, kuma bazan gode maka ba sbd bani na saka ba.“
yayi saurin sakin murmushi yace “dama badon ki gode min nayi miki sbd ba nema kikai ba martabarki ce kawai takai ayi miki abinda yafi haka.“
Na juya tare da cewa “kai dai ka jiyo“.
Sai dai a zuciyata ba karamin dadin kalamansa naji ba sbd ni mtm ce me son a zigani.
Na nufi inda mufida take wacce har yanzu ke zaune kawai tana kllnmu ta mike kai tsaye muka nufi class muka cgb da lacca.
*** Wato 2nda nake a duniya ban taba ganin mu2m irin saurayinnan ba, ya hadu ta ko‘ina kuma ba shakka yasan abinda yake yi kalamansa kawai ke tbbr da haka, abinda nayi iya kokarina na gano na kasa shine me yasa yake burgeni? me yasa yake da kwarjini a idona? me yasa bana iya wulakantashi kamar sauran mutane??? tambayoyin dana kasa bawa kaina amsarsu kenan ***.
Bayan kwanaki uku da faruwar haka, na shiga inda ban taba shiga ba library don duba wani littafi me danake ma2kar bukatarsa da wuri, al‘adata ban damu na duba littafi a library ba domin waya kawai zanyi a kawo min shima wannan din don ina bukatarsa da gaggawa ne.
Ni kadai ce a cikin wajen hakan yasa nake neman nawa ckn kwanciyar hankali, motsin shigowar da naji yasa nayi saurin dago kai

muka hada ido dashi nayi saurin dauke kai daga kllnsa, yadan tsaya yana kllna Ikc guda ya tako tare da cewa “Amincin Allah a gareki ya tauraruwar da haskenta baya disashewa“, ko kllnsa banyi ba naci gaba da abinda nakeyi, ya tako a hankali izuwa nesa kadan dani yace “nayi sa‘a kenan yau zan taya sarauniyar mata bincike me kike nema ne??“
ko kllnsa banyi ba nace “ Idon matambayi “.
Hmmmm lemme stop here kar mucika cikawa kuce yayi yawa..!
Ya kyalkyale da dariya yace “ kema fa kina da abin dariya gaki dai kamar ba zaki yi ba “, ya zauna a kujerar dake nesa kadan dani ya dora da cewa “nayi mamaki ma2ka dana duba kaf makarantar nan ban hango tauraruwar dake haska wannan makarantar ba ke kinga yadda duk makarantar tayi duhu kuwa??
akwai bukatar ki fita ko don ki haskata“.
Na dauke kaina daga Ittfan da nake dubawa nace “kai!! ina yin abuna a nitse kazo zaka rikitani wai kai wane irin mtm ne??
Kai baka rabo da NACI??
Baki, musulmi kuma bahaushe. Ya bani amsa irin wannan a karo na biyu sannan ya dora da cewa “ina da naci musamman idan ina so na isar da wani sako aka kasa fahimtata.
Na tabe baki nace “sako?? wanne irin sako kake so ka isar??“
Ya danyi shiru jimawa kadan ya mike alamar wasa ta fita daga fuskarsa yanayi na fadar magana da gaske ya shigeta ya taka a hankali izuwa gaba yace “ Akwai wata kalma da ake kira SO wacce a baya ban santa ba, ban fahimceta ba hasalima ban yarda da ita ba. Abinda na dauka shine ba zata iya tasiri akaina ba sai gashi Ikc guda na fahimci ashe SO gsky ne domin tamkar kwayar virus yake wajen saurin fadada, yana da ma2kar gudu a cikin jini hakan kesawa yayi saurin bin sassan jiki kwatankwacin yadda yabi jinina ya hana min duk wani sukuni....“
Nayi saurin jan wani dan karamin tsaki nace “

To ni ina ruwana?? “
Ya juyo izuwa gareni yace “abinda kika kasa fahimta shine na kamu da sonki duk da cewa ban sanki ba bansan daga inda kike ba hasalima ko sunanki ban sani ba, wannan na daga cikin aikin SO ba ruwansa da kyau, muni, asali ko kuma banbancin akida.
INA SONKI!!! kalmar da bana shayin fadarta a ko‘ina domin na tbbtr shine abinda ke ckn zuciyata.
Nayi saurin dago kaina idanuwana suka zaro tamkar zasu fado, Kana sona??
Tambayar dana fara yi masa kenan na dora da cewa “ Ban taba tsammanin jin wannan kalmar daga bakinka domin wadanda suka fika komai ma ba wanda ya taba 2nkarata da wannan maganar...“
hakan na nuna miki irin son da nake miki kuma yana tbbtr miki ni masoyi ne gaske bana yaudara ba.
ya fada kyakykyawar fuskarsa na kaina.
Na ajiye littafan dake hannuna na mike da dubeshi tare bata hade rai wanda ban taba yin irinsa ba nace “ kaga leader kake kowa?? wasanka yana yin yawa yakamata kasani akwai wasan da kakanni kawai ake yiwa irinsa....
Ya katseni da cewa “Wlh ba wasa nake ba idanuna kadai sun isa su tbbtr miki da haka, amsa kawai nake jira daga kyakykyawan bakinki wanda ta yiwu shine danbar fara sabuwar rayuwata“.
Amsa kake jira?? na tambaya ina kIlnsa nace “ kana tsammanin amsata zata zo a yadda kake so ne?? to kayi kuskure, babu wata maganar soyayya tsakanina dakai kayi gaggawar janye wannan maganar ko don tsira da mu2ncinka a idona.
ya gyara zamansa izuwa kallo na sosai yace “ Bazan taba janye kudirina ba sai dai idan har zaki fada min shin wani mummunan hali gareni da za‘a ki sona sbd dashi??
Na girgiza kai nace “ba wani mummunan hali

amma koba komai banbancin class... kuma ma kawai bana ra'ayin soyayya yanzu."
amma.............
Nayi saurin katse maganar tashi da tsawa nace "Bana sonka!! nace bana yi!! karka kara zuwar min da zan2ka irin wadannan sbd nafi karfin jinsu bare na yarda dasu."
Fuskarsa ta sauya ma2ka ckn yanayin da ban taba zaton akwai ranar dazai zama haka ba a yadda nake ganinshi, yace " Naji na amince kuma na hakura amma zanso kiyi abinda idan na tafi bazan zargeki ba sai dai na zargi kaina."
Kamar yaya?? na tambaya ina kllnshi.
Yace " kiyi min duk irin jarabawar da kika gadama a duniyar nan da kowacce nau'in tambaya kîka gadama idan har na fadi to shikenan na hakura kuma bazan taba zarginki ba sai dai na zargi kaina."
Idan kuma ka amsa fa??
Nayi saurin tambayarsa.
Yace "sai ki dauki kaddara ki yarda muyi soyayya.
Na bishi da kallo na koma inda nake a baya na zauna nace " ba tambaya daya zanyi maka ba sai dai guda uku kuma cikin kwanaki uku a jere idan ka fadi a daya ko kayi tsallaken rana daya shikenan dole ka rabu dani."
Na amince.
Ya fada ba tare da jinkiri ba....
Na bishi da kallo ckn mamakin yadda bai tsorata da komai ba saima wani karfin gwiwa da yake da ita, ya tsareni da ido jiran irin tambayar da zanyi masa kawai yake.
Allah ya sani yana ma2kar birgeni sbd ya hadu sai dai kawai ji da kai da takamata ta hanani na amince da ainihin abinda ke zuciyata, wacce tambaya ma yakamata nayi masa?????
Tambayar dake ta yawo a zuciyata kenan ckn salo na nazari.
Zuwa can na dago kai nace "tambayar yau me sauki ce ina so ka canki sunana wanda mahaifina ya rada min, sau daya kawai zaka

fada idan ka fada ba dai-dai ba ka fadi.“
Yabi ni da kallo tare da gyara zama yace “ Sunanki?? Haba ranki ya dade ta ina kika taba ganin an fadi sunan mtm daga ganinsa??? SUNAYE na daga abubuwan da suka fi komai yawa a duniya don haka amsa wannan tambayar is impossible a ko‘ina, a zatona zakiyi min tambayane wadda kwakwalwa zatai aiki wajen gano amsa amma ba canke-canke ba.
Na danyi gun2n murmushi nace “daga farawa harka fara karaya?? wannan itace mafi sauki daga wadanda nayi maka tanadi, koka manta kai kace duk irin tambayar da nake so??“.
ya kauda kai daga kallo na a hankali ya dan jima baice komai ba zuwa can yace “bari kwakwalwa tayi aiki“.
Ya mike daga inda yake zaune ya fara takawa a hankali yana kaiwa da komowa hade da kallona a wasu lokutan, yanayin na nuni da zuzzurfan nazarin daya shiga, ni kuwa har wani murmushi nake yi idan na kalli halwar daya shiga, yau dai zan rabu da kaya.
Abinda naketa darsawa kenan domin ina da yakini 100% bazai iya amsawa ba.
y‘an min2na kalilan ya kwashe ya juyo gareni yace “A mafi yawan lkt suna nayin tasiri a kamar mu2m da yanayinsa, idan har an sami haka a kanki to ina da tbbcn sunanki ba me guda daya bane irin sunan nan me guda biyu ko ince tagwaye kamar “fatima-bintu, zainab-abu, halimatus-sadiya! sai dai duk bakiyi kama da wadannan sunayen ba.
Ya dan taka da kafarsa dake sanye da wani kyakykyawan farin takalmi ya juyo gareni ya kalleni na dan lkc yace
“AISHA HUMAIRA!!!!!!!“
Ya fada tare da sake mai-maitawa da fadin “yes nafi yarda sunanki Aisha humaira....“ ya zarce da kllna don jin abinda zan fada.
Ni kuwa 2ni idanuna sun kwalalo waje sbd AL‘JABI, ya akai kasan sunana??
tambayar dana jefa masa kenan, fuskarsa

tadan fara saki yace “ kina nufin Na fada dai-dai kenan??“
Bansan sanda na gyada kai alamar eh ba, ya kawo gwauron numfashi hade da murmushi ya koma ya zauna tare da cewa “Step one done saura na gaba, ita dama SOYAYYA hadin Allah ce idan yaso koke baki da ikon hanawa kuma ina da yakini da karfin gwiwar yin nasara sbd ina ji a jikina akwai alkhairi a tarayyarmu.“
Ya mike tare da ja da baya fuskarsa cike da yalwataccen murmushi yace “Nima sunan nawa me tagwayene UMAR FARUK!! sai an jima farar tauraruwa me farin haske.
Ya juya ya fice.
Na daki tebirin dake gabana kamar na fashe da kuka, gsky ya birgeni amma naji haushin yadda yayi kaca-kaca da tambayata mafi tsauri irin wannan domin ba canka kawai yayi ba hankalinsa ne yayi aiki a wurin.
wai wannan anya kuwa mu2m ne???
dakyar na karasa abinda nazo yi na tafi class.
°ranar sai ya zamana duk na zama wata iri 2nanin irin zazzafar tambayar da zanyiwa faruk kawai nake wacce zata gagareshi amsawa, koda ace zan yarda da soyayyar faruk amma bana so ya kureni, sai dai duk tambayar data fado min sai naga kamar kwaf daya zaiyi mata°
Washe gari 2nda na shiga makarantar bamu hadu dashi ba har aka tashi na fito daga class na hangi driver na sai dai dole na jira mufida wacce bata fito ba har yanzu, na karasa jikin motar na bude bayanta na zauna ba tare dana rufe kofar ba saima kafafuna dana ziro waje, salon sallamar dashi kadai keyi tasa nasan ya iso, na dauke kai kawai.
Ya dubeni sosai yace “sorry for the late, Allah ya taimakeni baki tafi ba da shikenan na fado ina fatan dai baki manta tambayar da kika tanado min ba??
Na kalleshi nace “bana so saina kayar dakai ta karfin tsiya ka hakura kawai zaifi maka sauki daga jin tambayar da miliyoyin mutane suka

gaza amsata masu ji da basirar, hikima da hazakar da tafi taka..Mai-makon kalaman yaudarar da nake amfani dasu suyi tasiri akansa saima ya kyalkyale da dariya ya dan taka kadan izuwa jikin kofar motar dana bude ya dafashi da daddadar muryarsa me ratsa zuciya yace “Humaira kenan kada kiyi tsammanin kautar da 2nanina akan abinda nake so kuma nake da yakinin zan sameshi, na kasance ina da baiwar yin abubuwan da miliyoyin mutane suka kasa, wannan kamar a jinina ne don haka karki damu kiyi min kawai ni abinda na dauka shine abinnan da muke yi kamar istahara ne a gareni indai tarayyarmu dake alherice to zan amsa tambayoyinki koda sun kai 100, idan kuma babu alheri a ckn soyayyarmu to bazan taba iyawa ba.“
Nabishi da kallo kawai nace:
*“ Akwai wata halitta a doron kasa wacce yanayinta ke caccanjawa.
Idan tana karama tana tafiyane da kafa hudu, idan ta girma kuma sai ta koma tafiya da kafa biyu, yayin da kuma ta tsufa sai ta koma tafiya da kafa uku, wacce halitta ce wannan???
*
Yayi saurin sakin kofar daya rike yabini da wani irin kallon da ni kaina sai dana tausaya masa, yaja da baya kadan Ikc guda ya fara kaiwa da kawowa a wajen hankalinsa in yayi dubu ya tashi, na saki yalwataccen murmushi nace “kaga faruk ba iya amsawa zakai ba ka.......“
Ya daga min hannu yace “ karki katseni “.
Na daga ido tare da tabe baki a raina nace ‘ayi dai mugani‘.“
Ya dan dakata kamar zaiyi magana sai kuma ya fasa ya shafi gashin kansa yace “DANKARI!!“
Na kyalkyale da dariya kawai na dauke kai na fara latsa wayar dake hannuna sbd a yadda nake ji a jikina na gama dashi, sai dai ta ciki na ciki don kuwa kirjina dif-dif kawai yake don bansan yadda zamu karke dashi ba. tsawon

Ikc muka shafe amma babu alamun ya karaya da amsa tambayar saima dada kaimi da yake wajen 2nani da nazari, jim kadan yadan yi nuni da hannun tare da gyada kai ya saki murmushi kyansa ya kara fitowa, ya tako a hankali izuwa inda yake tsaye 2n dazu yace:

“ idan har 2nanina da nazarina sun bani dai-dai-dai to ina da tbbcin ba kowacce halitta bace wannan face MUTUM wato bil‘adama.dalili kuwa mu2m sanda yana yaro da kafa hudu yake tafiya shine RARRAFE, gwiwoyi biyu hannaye biyu.

Yayin kuma daya girma ya iya tafiya sai ya koma tafiya da kafa biyu kamar yadda ni dake muke tafiya yanzu.

Lokacin kuma da mutum ya tsufa sai ya zamana kafa biyu ba zata iya daukarsa ba sai ya kara da sanda a matsayin kafa ta uku.“

Bansan sanda wani irin murmushi ya kwace min ba wanda shine ya nuna ainihin abinda ke zuciyata nake dannewa, yadda yake zano abubuwan tamkar me karantawa a littafi ya birgeni ma2ka.

Shima yayi murmushi tare da cewa “ zan iya cewa wannan murmushin tayani murnar cin nasara a karo na biyu ne??“

Na gyada kai tare da cewa “kwarai kuwa da alama gaf kake da cina da yaki faruk akan haka dole na jinjina maka domin kaine mu2m na farko daka fara neman ka kureni, murmushin da kaga nayi na tayaka murna ne da kuma tausaya maka domin ka kai matakin da dole kayo kasa domin gobe koda kai aljanine baka isa ka amsa tambayar da zanyi maka ba.“

Ya dago kansa ya fashe da dariya yace “kina birgeni sarauniya sbd komai naki me tsari ne kuma da karfin gwiwa hakan na daga ckn abinda yasa muka dace da juna, idan wai kina tsorata nine to sai ince miki kima hutar da kanki don kuwa ma2kar ina tuna cewa soyayyarki nake nema to zanyi abinda aljani ma bazai iya yi ba.

Na gyara zamana dai-dai sanda na hangi mufida tare da kokarin shigo da kafata ckn motar nace “can dai da yawarka“.
Yayi dariya ya gyara doguwar jakar dake rataye a kafadarsa wadda ta hadu da dressing din jikinsa tayi masa kyau yaja da baya a hankali yace “Ki shiryawa fara sabuwar soyayya a gobe......“ Nayi saurin katseshi da cewa “ko kuma ka shiryawa bakin cikin faduwarka a gobe ba“. Ya dan dakata yace “ to shikenan zan iya cewa duk mu jira FINAL din don ganin yadda zata kaya, ya dora hannunsa a gefen goshinsa ckn alamu na sarawa tamkar soja yace “sai gobe farin ganina“...
Hmmm mumadai allah yakaimu GOBEn muji wannan wata tanbayace haka..zata hada ko zata raba..?!
Mufida na isowa direban wanda har ya fara barci na daka masa tsawa ya farka ya juyar da motar muka nufi hanyar da zata sadamu da gida, Mufida ta dubeni tace “amma fa nayi mamakin yadda naga kuna hira da faruk harda dariya sai kace ba ke ba??“
Na kwantar da kaina kadan nace “manta da wancan faruk din lamarinsa sai shi.“
mufida tayi dariya tace “Ah kidai fadi gsky tbbs akwai wani abu“.
Ganin yadda take kokarin kureni yasa na kautar da zancen ban bari yayi nisa ba, har na isa gida.
*Abinda na kasa ganewa game dani shine: Nidai faruk na birgeni ma2ka, komai nasa naban sha‘awa, shine kawai a duniya da bana iya tozartawa ko in wulakantashi koda nayi niyya sai hakan ya gagara yiwuwa a wajena. Ga yawan 2naninsa da nake yi a koda yaushe banda son kasancewa dashi a kowanne lkc da nake yi!! Shin wannan shine SO?? tambayar dani bansan amsarta ba kenan.*
Washe gari misalin karfe tara na safe tsaye nake a jikin wata faffadar bishiya dake harabar makarantarmu nesa kadan da inda dalibai ke

zama, kasancewar yau an tashi da lullumi ga iska me dadi na kadawa yasa nake jin dadin wurin.
Gefe guda dalibai ne group-group masu hira nayi masu kara2 nayi, Ni kuwa littafine a hannuna ina karantawa hankalina gaba daya tafi ga kara2n, jin sallamarsa yasa dole na tsagaita daga kara2n da nakeyi duk da cewa ban dago na kalleshi ba.
Amincin Allah a gareki ya maʻabociyar son kadaici da hutawa, Ya fada 2n yana nesa kadan dani. Dan kwalisan saurayi kllm kara kyau yake ya karaso inda nake tsaye yace “ina fatan dai kin shirya tambayar dazan bige a karo na karshe??? Nayi banza kmr banji abinda yace ba. Yayi murmushi yace “ Kinyi shiru kodai kin karaya ne??
Nayi yaken karfin hali nace “baka isa kasa na karaya ba, yau so nake ka fada min ranar da aka haifeni da watan da shekarar kayi jumulla ka fada min shekaruna nawa??
da wata nawa??
kuma da kwana nawa??
Nayi karatu a kasar waje ka fada min wace kasa ce kuma wacce university??
Na kumbura baki sanda nakai karshen maganar ckn gadara da takamar cewa na gama dashi.
Ya kura min ido kamar baisanni ba.
na kalleshi nace “yadai ka kasa cewa komai kodai ka karaya ne??“
Yayi murmushi yace “gskyrki da kika ce ko aljani yayi kadan ya amsa tambayarki tayau sbd shima baisan gaibu ba amma ina so ki sani SOYAYYA ba karya bace don haka duk abinda naji a jikina game dake to gskyne, zuciyata bata taba gaya min karya akanki ba don haka zan jaraba idan har son gsky nake miki na tbbt Allah zai bani nasara.
Ya taka kadan gaba da inda yake yace:
Irinku rayuwarku na tfy ne ckn tsari ba a hargitse ba don haka ina da tbbs idan nace, an saki a primary shekara shida sannan kika

samu shekaru shida a ita primary din, kin secondary da shekaru 12.
kika gama secondary da shekaru 18 kika wuce university kika yi shekaru 3, jumulla shekarunki ashirin da aya (21) yanzu.
Tofa!! 2n daga nan idanuna suka zaro waje sbd AL'AJABI.
Ya kara gyara tsayuwa yace "idan har jikina dai-dai yake bani an haifeki 1/6/1994 kuma kinyi kara2 a OXFORD UNIVERSITY ta kasar england domin itace burin duk wani dan gata irinki."
Hmm... Nifa tun kafin ma yakai karshen zancen nasa bansan sanda duk abinda yake hannuna ya subuce ba naja da baya a dan tsorace, idan har faruk ba aljani bane to yana harka da aljanu.
Kallo daya yayi min ya tbbr ya amsa dai-dai ya tako inda nake tare da durkusawa ya tattaro kayana da suka zube kasa ya mike muka fuskanci juna yace "karki AL'AJABI ko mamakin abinda ya faru a maimakon haka ki yarda Allah keson tarayyarmu, nasan kina sona tun tuni don na dade da gani a idanunki amma kina dannewa abnd kika manta shine zuciya ba'a yaudararta akan soyayya yau dai wasa ya kare zamuyi soyayya abar kwatance indai da tsawon rai.
na karbi laptop dina da littafina harma da wayata daya miko min yaja da baya yace "Yes ki shirya daga yau an fara, I LOVE YOU."
ya juya izuwa ga abokansa dake can gefe nesa sosai da inda nake, nabishi da kallo kawai na kwantar da kaina a jikin bishiyar da nake, wani murmushi ya kwace min Allah ya sani ina so kauce-kauce ne kawai irin nawa yau kuma karya ta kure.
Nadan dade ina cgb da tsayuwa a wurin har zuwa sanda lkcn shiga class, ko break yau ban fito ba yau sai da aka tashi na samu naja mufida bamu bata lkc ba muka tafi, kai tsaye gd muka nufa bayan da muka sauke mufida a gdnsu.

Isowata keda wuya da yake da yunwa na dawo kai tsaye kitchen na wuce na zubo abinci naci nayi sallar azahar sannan na jawo laptop dina na shîga aikina. Zaune nake bisa luntsumemiyar kujerar falon namu na tankwashe kafafuna laptop din na ajiye bisa cinyoyina gaba daya hankalina ya tafi ga laptop din sai shiga da fita nake, television dake yi ma kasheta nayi sbd karar ta dameni. Tunda na fara ba kakkautawa sai naji an kira sallar la'asar sannan na rufe na sakko tare da shimfida darduma na jawo katon hijab dina dana tanada musamman don yin sallah nasa. Idarwa ta keda wuya momi ta fito falon ta zarce izuwa kujera ta zauna ta danna remote din dake rike a hannunta tafkekiyar T.V din dake manne a jkn bango ta dawo taci gaba dayi. Gamawata keda wuya na mike na koma kan kujera na zauna na jawo laptop dina na budeta, momi tace "aikin kenan bakya gajiya bakya daga kafa." Na danyi dariya nace "momi ai computer tayi, uhm don Allah momi dan rage karar t.v dinnan tana takura min, momi tace "don kina wannan shiririitar sai nabar jin abu me muhimmanci irin wanda nake kll yanzu??"
Nadan kumbura baki nace " momi shiririta kuma??"
Eh an fada shiririta ai ni wannan makarantar taki da ita da shirme duk dayane a wurina."
Na dan hade rai nace "ai kuwa momi ba shirme bace don kara2n computer na daya daga ckn mafiya tsada a duniya, kuma wlh yadda nake jin dadin makarantar nan ko OXFORD banji dadinta haka ba."
Momi ta kauda kai tace "karyar banza!! yanzu dai ki tashi kije banki ki ciro min kudi zanyi baki gobe ba kudi a hannuna kinsan dadynki sai jibi zai dawo," Na dan cilla hannu nace "kayyyy!! momi kina gani aiki nake yi kuma....."
Ta katseni tana kallona da cewa "OK ba zaki je ba kenan???"

Na mayar da kaina ga laptop din dake gabana
nace “Zanje“
to ki tashi maza ki tafi kinga yamma nayi, na
rufe laptop dina na nufi dakina kai tsaye
bathroom na shiga nayi sabon wanka na wuce
ma‘ajiyar kayana na saka wadanda suka dace
dani a yanzu na dawo ga tafkeken madubina
na zauna kujerar dake fuskantarsa zagaye dani
kayan kwalliya ne bila-adadin kala-kala.
Bayan dana gama shiryawa na kalli kaîna
bansan sanda wani murmushi ya subuce min
ba, hmmm... wato ba karya ne ba ni nakai
mafi kololuwa fagen kyau bama kyau kawai ba
komai nawa daban ne domin abinda kesa
wasu muni ni kuma kyau yake kara min bare
kuma nasa abu me kyau, Na zama
kwatankwacin zarah a ckn taurari gasu da
yawa amma daka daga kai ni zaka fara gani.
Na fito izuwa harabar kasaitaccen ygdn namu
ina takun isa, takama da gadara.
Direba ya taso da gudu tare da cewa “ranki ya
dade ina zuwa haka??“
Na harareshi nace “Ba ruwanka da yinda zanje
bani mukullin waccan motar,“ nayi nuni da
CR-V din dake nesa kadan dani.
A tsorace ya miko min tare da cewa
“amma.......“ Nayi saurin katseshi da tsawa
nace “Yau nizan tuka kaina inda nake son
zuwa ka koma kuci gaba da zaman
munafuncinku, na warci mukullin daga
hannunsa na shige motar na juyar da ita na
fice nabi titin dazai sadani da inda zanje.
Tafiyar min2na 15 nayi na iso katafaren bankin
nayi parking motata a inda aka tanada na
wuce ckn bankin, Al‘adata duk sanda nazo kai
tsaye wajen manager nake wucewa ya 2ra a
ciro min abinda nake so in juyo na fito sbd
asalinsa yaron dadyna ne.
Zuwana ofis din nasa dai-dai inda ya saba
zama nayi turus don yau wanda nake
tsammani bane ba abinda yafi kenan ba wanda
ke zaunen 2n daga zamansa dress dinsa da
komai nasa ma nasan ko waye.

Na tsaya akansa nace “ Ah!! Ya haka kuma?? Dalibi a wani wuri ma‘aikaci a wani wuri?? Faruk ya dago kai koda ganin nice sai ya saki murmushi ya gyara zama yace “ kina mamaki ne??
Na gyada kai dai-dai sanda na zauna a kujerar dake fuskantarsa nace “yes!! dole da mamaki mana kodai faruk din biyu ne bayan wanda na sani??“
Yayi dariya yace “Nine dai wanda kika sani don ba sunana husaini ba bare kice hassan dina kika gani, dama kina zuwa nan ne?? Ba tare dana dubeshi ba nace “shi yasa ma nake mamakin ganinka don ban taba ganinka anan ba sai yau.“
Eh gsky ba zaki ganni ba sbd ba anan bangaren nake ba yau ne kawai na dawo nan as temporary time kafin me kujerar ya dawo ya karbi wurinsa, ya dago idonsa yace “cire kudi, turawa ko kuwa kawai yawon shakatawa???“
Na dan yi dariya nace “Ah haba yawon shakatawa a banki kuma?? Bama dai zaka ji abinda ya kawoni ba......
Me yasa?????
Ya tambaya yana dubana.
Nace “sbd ba wajen ka aka turoni ba wanda aka 2roni wajensa baya nan kaga kuwa a matsayina na y‘ar aike dole na koma na fada idan ance na dawo wajenka na dawo!!“
Yayi murmushi yace “Nima zanyi farin ciki ki koma din 2nda na tbbr idan aka tambayeki wa kika tarar zaki ce masoyinki FARUK kika gane a wajen, kinga ko tanan na fara samun shiga a wajen momi da dadynki.“
Na zaro cak a jakata da biro na dora a tebirin dake gabana na fara rubutawa nace “Tayaya kake tsammanin zan fadi haka???“
Sbd nasan ba zaki taba yin karya ba.
Na tura masa cak din bayan dana gama rubutawa ya kira wani jami‘in banki ya umarceshi daya je ya ciro min kudin muka cgb da hira ckn nishadi, Na dubeshi nace “Lallai

bayan kokari ma harda daukan dala ba gammo kake yi, AIKI irinna banki + KARATU irinna computer ba hu2 kenan???"
Ya kwantar da kansa jikin kujerar da yake kai yace "Aikin ne ya jawo kara2n kuma duk tare suke tafiya basu shiga lokacin hutu ba, Muna da rauni ta bangaren masu ilmin computer shine dalilin da yasa aka 2rani na karo sani akanta don cgbn wannan bankin, kinji dalili."
Na bishi da kll nace "yanzu na gano dalilin da yasa bana ganinka in nazo, wato dan lele ne kai a bankin." ya daga kai yace "of course kamar yadda na zama dan lelen zuciyar humaira.
Nayi saurin girgiza kai nace "Waye ya gaya maka? Baka samu wannan damar ba ba kuma zaka taba samu ba har abada sbd ni zuciyata FARUK ne kawai a cknta kuma daga shi na rufe ba wanda zan sake bawa dama ya shiga bare ma har yayi tasiri."
Ya dan lumshe ido ya dago kai yace " faruk na godiya hade da alkawarin rike amana bata shekaru kawai ba ta HAR ABADA."
Na jinjina kai nace "A wasu lktn alkawari nada saukin dauka amma saukewa nada ma2kar wahala".
Ya gyara zama yace "Ina da tbbcn duk nauyin alkawari ma2kar ke na daukowa shi to zan sauke sbd ni akan SOYAYYA..... ni kaina mamakin kaina nake yi."
Na bishi da kallo kawai, nima na dade da yarda yana da zafin soyayya, jim kadan jami'in nan ya dawo ya dora leda bisa tebirin dake gbnmu tare da cewa "Sir, gasu an ciro."
Ok thank you, koma bakin aikinka.
Ya 2ro minsu yace "An cika aiki."
Na kauda kai nace "OK a takaice dai kora ta kake ko??"
Ya girgiza kai yace "Mezai sa na koreki?? Alhalin kece fitilar dake haskawa zuciyata hanyar daya kamata tabi?? Gani dai nayi kawai kin samu abinda ya kawo ki."
Na juyar da kujerar da nake kai izuwa gefe

nace “Amma ban gaji da kIln faruk ba“.
Yayi murmushi yace “Shima bai gaji da ganinki ba sai dai idan kuka kwantar da hankalinku wannan rabuwar ta wucin gadi ce domin zaku hadu a rayuwa ta har abada.“
Na saki murmushi kawai.
Yayi saurin matsowa gaban kujerarsa yace “yauwa ni kuwa na manta ban karbi lambar sarauniyar tawa ba, na dago wayar dake hannuna kaina na kanta nace “ Ai da farko na zaci itama zaka canka ne 2nda shi yafi komai sauki a wajenka.“
Yace “Eh don dai kawai idan kika bani da kanki zata fi martaba ne a idona, amma da sai dai kawai kiji kira.
Na 2ra wayata izuwa gabansa nace “ai ko ifritu ba yadda zaiyi ya canki lambarnan dai~dai.“ Yayi dariya kawai ya 2ro min wayoyi biyu na dauki tashi lambar na mike tare da rakiyarsa na fito daga bankin.
Na dubeshi nace “kaga me girma manager nifa bance kayi min rakiya ba.
Yayi murmushi yace “bai dace ba ace sarauniya kamarki tana tafiya babu dogari ko daya a gefenta.“
Na girgiza kai nace “A yanzu ai ba sarauniya da dogari bane ke tafiya, SARKI da SARAUNIYA ne.“
murmushi ya fadada a fuskarmu har zuwa sanda muka karasa jikin motata, ya bude kofar gaba tare da dora hannunsa a goshinsa ckn salo na sarawa tamkar wani soja yace “shiga da Ify tauraruwar taurari.“
nayi murmushi kawai na shiga na zauna ya mayar da kofar ya rufe da yake glass din a sauke ya dafa kofar da hannunsa biyu yace “murmushinki ya dace da fuskarki kwatankwacin yadda ni dake muka dace da juna, sai mun hadu next time farin ganina.“
Ya juya ya koma ckn bankin nabishi da kallo murmushi na tashi a fuskata har sanda na daina ganinshi a hankali na daga glass din motar tare da takata na nufi gd.

Wannan shine tarihin asalin fara soyayyata da FARUK.
************ ************ ****

Daga ranar ne kwanci tashi alakarmu na kara karfi har takai soyayya me karfi ta shiga tsakanina da FARUK wadda tafi gaban a kwatanta, har takai mun zama ababan misali domin bawai tsakaninmu kawai ba kowa yasan alakarmu da kuma karfin syyrmu.“
Musamman a makarantarmu wanda kowa yayi mamakin ganinmu tare rana tsaka muna soyayya tamkar bani ba, daga nan ne kuma na zama ta mutane muka fara kulla abota da mutane daban-daban ta silar faruk.
Ban taba jin son wani bil‘adama a duniya kmr FARUK ba kuma ban zaci zan tsinci kaina a hakan ba, takai ga bana iya yi masa musu a duk abinda ya fada, bana ganin rashin dai-dainsa a duk abinda yayi, Sa‘a daya da nayi da shima yana ma2kar sona domin idan son da yake min baifi nawa ba to nawa bazai fi nasa ba.
Kasantuwar kusanci da karfin syyrmu yasa har aka fara kiranmu da sunaye daban-daban wasu suce LAILA da MAJNUN, wasu suce ANGELICA da MACIOLA dadai sauransu.****
FARUK ya kasance haifaffen garin kano kmr ni, ckkken sunansa UMAR FARUK MUHAMMAD yayi primary, secondary da university duk a garin kano, ya karanci irin abnd na karanta mathematic economics a BUK. Lbrn rayuwarsa daya bani wanda nafi tausaya masa shine kasancewarsa maraya.
Ya rasa mahaifansa 2n yana karami ta silar hatsarin mota, ya taso ne a hannun kishiyar mahaifiyarsa me suna hajiya amina, yana yawan ambaton sunanta a koda yaushe domin a cewarsa itace gatansa a duniya ita zame masa uwa da uba ta rikeshi tamkar dan data haifa a cknta har izuwa yanzu.
Ni kaina na yaba da halayenta da kirkinta ranar farko da faruk ya kaini gdnsu muka gaisa da ita, ba shakka yayi sa‘ar samunta

matsayin wacce ta rikeshi har izuwa grmnsa.
A duk ma'aikatan gdnmu ba wanda baisan FARUK ba domin sai da takai idan direba yakai ni makaranta FARUK ne ke dawowa dani a motarsa sannan ya wuce, kai harta da momi ma tasanshi kuma tayi farin ciki da ganinsa ta yaba dashi sosai duk da ban fada mata ba amma ta fahimci abinda ke tsakaninmu.
Kwanci tashi har lokacin gama makarantarmu yayi bayan tsawon lkc da muka shafe, ranar karshe ta rufe laccarmu bayan mun fito na nemi faruk banganshi ba mufida kuwa na can ckn kawaye suna irin sallamar nan tasu ta kawaye, nima nayi sallama da iya wadanda na sani da yake yunwa nake ji kai tsaye restaurant na dosa domin gani nake kmr bazan iya kaiwa gd ba, zamana keda wuya na umarci dan matashin saurayin dake jigilar kawo abinci na gaya masa abinda nake so ya kawo min.
A hankali FARUK ya karaso tare da zama a kujerar dake fuskantata ya dubi me kawo abincin tare da cewa "kai kawo min abinci da sauri."
Na dubeshi nace "wane irin a kawo maka abinci baka ga na riga ka bane??"
Ya dubeni ya tabe baki yace "ina ruwana ni??" ya juya gareshi yace " kai aje a kawo min ka taho da juice me sanyi."
Na kara hade rai nace "baya yiwuwa wlh na riga ka don haka dole ni za'a fara kawowa."
Me kawo abincin ya tsaya kawai ya kasa tfy ya dubemu yace "to ai ni na rasa yadda zanyi daku ai duk kun rudani, pls daya ya hakura a fara kawowa daya mana."
Faruk yace "kai manta da ita dallah jeka kawo mana."
Kayiwa Allah ka juya ka tafi karka yarda ka kara kusanto inda nake sbd ni yanzu bani kadai bace tafe nake da rakiyar KADDARA, yayinda BALA'I da MASIFA ke take min baya.
Yayi saurin girgiza kai yace "Ba wata kaddara da zata iya sawa na gudu na barki, karki manta Alkawarinmu na kasancewa a tare duk tsanani duk wuya.
Da ace ba wata masifa da zata iya riskar dan adam toda har abada ba za'a taba iya gane masoyi na hakika ba, sai kaddara ta afku ne kawai ake iya gane soyayya ta zahiri da kuma ta karya don haka yanzu ne yafi ko yaushe cncnta na nuna miki soyayya."
Na daga kaina sama wasu sanyayan hawaye suka gangaro min, ya tako izuwa inda nake ya durkusa ya dafa keken da nake kai yace "Sannan idan zaki 2na na taba gaya miki cewa ba ina sonki don wani abu naki bane ko don moruwar wani abu daga gareki, ina sonki ne a matsayinki na humaira kuma zanci gaba da sonki har abada."
Ya mike tare da duban daddy yace "Idan har ka amince ni zan auri HUMAIRA a haka, zan zauna da ita domin bazan taba guje mata ba har abada.
Babu bukatar duniya tasan abnd ya faru da ita bare makiyanmu su sami bakin yi mana dariya.
Fuskar daddy tayi saurîn washewa, wani sbn annuri ya saukar mata ya mike tare da cewa "Lallai faruk ba'a banza ba humaira ta yarda da kai yau na gani da idanuna don nayi imanin ko ni ban fika son humaira ba, laifi nane da

nayi yunkurin hana abnd Allah ya kadarta.
Nagode da kayi yunkurin rufa min asiri da kuma masoyiyarka.
Lallai samun masoyi kamarka za‘a dade ana tonawa.“
Faruk ya gyara tsayuwa yace “Don na rufawa HUMAIRA asiri ba wata bajinta nayi ba domin kaina nayiwa.“
Daddy ya gyara babbar rigarsa yace “idan kuwa har kayi min haka nayi Alkawarin baka dukiya me tarin yawa kuma zan dauki nauyinku kai da ita ba abnd zaku nema ku rasa.“
Faruk ya girgiza kai yace “bana bukatar komai daga gareka indai akan HUMAIRA ne sbd daga ranar da na samu humaira hakkin kula da ita da samar mata da farin ciki akaina yake kuma dole na saukeshi.“
Daddy yayi saurin cewa “uhm!! kaji masoyin gaske masoyi na hakika yanzu kai kana ganin a shirye kake??“
Faruk ya gyada kai yace “kwarai kuwa!! abinda kawai nake so a dauke daurin auren daga gobe a matsar zuwa jibi idan zai yiwu.“
Ah! kwarai kuwa sosai ma!!
Don dai kwana daya kawai??
Faruk ya kada kansa tare da juyowa muka kurawa juna ido, ni kaina ya bani mafi girman mamaki a yau, domin duk yadda nake hango HALACCIN faruk ya wuce nan.
DAN HALAK farar fuska farar zuciya.
Har yanzu hawaye ke kwararowa daga idanuna har na fara hango yadda sabuwar rayuwarmu zata kasance duk da cewa bata zo mana a yadda muke so ba.
Ya goge hawayen dake idonsa har ya taka izuwa bakin kofa sai ya juyo yace “kayi hakuri amma Sai kasa an kwashe wadancan gardawan banzan daka tara a bakin gate izuwa asibiti sbd ta karfin tsiya na bigesu na shigo nan.“
daddy yayi saurin gyada kai yace “KARKA DAMU KAYI DAI-DAI.“

Ya juya tare da yimin klln karshe ta wani irin salo kmr zaiyi magana amma sai ya fice, nabi daddy da kll na durkusar da kaina na fashe da kuka kmr raina zai fita.
Kukan na abubuwa da yawa ne da suka cunkushe zuciyata, ko yunkurin rarrashina ma ba wanda yayi zuwa jimawa MUFIDA tazo a lkcn ina daki ta zauna a falo momi ta zayyane mata duk abnd tijjani ya fada da tsananin mamaki ta dago kai tace “amma TIJJANI anyi tsinannen mu2m mara mu2nci da bashi da imani a zcyrsa, ynz momi shikenan komai ya rushe???
Ta girgiza kai tace “FARUK yazo kuma yace yaji ya gani ya amince ba abnd za‘a fasa, sai dai nifa ina jin tsoron al‘amarin nan sosai.“
MUFIDA tadan yi gun2n murmushi tare da girgiza kai tace “babu abin tsoro momi, 2nda nake ban taba ganin soyayya irin ta HUMAIRA da FARUK ba, wlh momi yadda kika san da son junansu aka haliccesu 2n fil‘azal.
A kyalesu kawai tbbs da abinda Allah yake nufi a tryyrsu.“
Momi ta kauda kanta kawai ba tare data sake cewa komai ba, mufida ta mike ta nufo dakina.
Kwance nake na kishingida akan makeken gadona na zubawa kafafuna ido hawaye na zuba daga idanuna, mufida tadan rufe min ido tare da bina da kll tace “haba HUMAIRA meye haka??
kuka bashi da wani muhimmanci a gareki sbd bai isa ya dawo miki da abnd kika rasa ba, a zatona farin ciki zan tarar kinayi Allah ya kadarta abnd kike buri.“
ckn sheshsheka nace “Dole nayi kuka sbd shi kadai ne abnd zan iya yi a yanzu, ba haka naso rywr aurenmu tazo mana ba.“ Shi kuma Allah haka yaso.
Tayi saurin fada tare da dorawa “Allah na tsara abubuwansa ne yadda yaso ba wanda ya isa ya canjasu, amma dai na tbbtr ko a yayane zakiyi dauwamammen farin ckn zama da faruk wannan kawai ya wadatar.“ Haka dai kalamai

irin nata na RARRASHI tayi ta jerowa.
*Faruk kuwa isarsa gida keda wuya ya fadawa wadda take uwa da ubansa kudirinsa da kuma taimakon da yake so tayi masa, duk da cewa bata fiya fushi ba amma a wannan karon sai data canja.
Tabishi da kll tace “A zatona kana da hankali amma ka canja.
HUMAIRA ce kadai mace a duniya??
ka manta abnd suka yi maka kenan??
sai yanzu da suka shiga wani yanayi sun kada gabas da yamma basu da me rufa musu asiri shine suka taho wurinka kai sbd kafi kowa wauta ka yarda ko??
kai wannan bai zama abin kunya bama a gareka??
Mutumin nan bakai kawai ya wulakanta ba harda iyayenka wadanda su zasuyi maka wakilci su kuma dame zaka 2nkaresu da yarda su dawo su shige maka gaba??
2n wuri ka cire wannan daga ranka don bame yiwauwa bane.
Fuskarsa ta canja kmr ya fashe da kuka yace “amma ummi mahaifinta ne yayi mana laifi ba humaira ba, ni kuma yanzu humaira nace zan aura ba mahaifinta ba laifin wani yana shafar wani ne??
Ta dan zaro masa ido tace “EH yana shafa! indai ina na isa na fada ka dauka to ka rabu dasu da y‘arsu idan a jibin kake son auren ni ina da wadda zan baka gasu nan da yawa ma.“
Faruk yayi saurin girgiza kai yace “ni HUMAIRA nake so ita zan aura kota yaya ni naji na gani 2nda ni zan zauna da ita.“
Ta daga kai sama tace “TO!! tashi daga kasa ka dawo kan kujera muyi magana 2nda ka zama abokina.“
Ummi ba haka nake nufi ba amma...
Ta katseshi da fadin “wai Yaushe ka koyi musu da gardama irin wannan to bani da lkcn musayar zance akan maganar banza tashi ka tafi.“

Dole tasa ya mike ckn nuni da hannu yace
“don Allah ummi ki.....“
Ka bacemin nace ko??
Ta katseshi.
Ya saki hannunsa kawai ya bita da kallo
kawai.
“Allah ya wuci zcyrki.“
Ya fada sanda ya wuce izuwa sashinsa,
bangarene me zaman kansa da falo guda gefe
guda kuma ga dakinsa gdn nasu dai-dai
gwargwado na rufin asiri ne.
Ya zauna jim kadan ya zaro wayarsa ya lalubi
lambar bbn abokinsa NAZIR yana dagawa yace
“kazo gida don Allah yanzu ina son ganinka,
...........
Ah lfy kadai zo yanzu.
................
OK sai kazo.
Ya mike ya wuce dakinsa min2na kadan yaji
motsin zuwan nazir yana fitowa nazir wanda
2ni ya dare kujera yace “HUMAIRA!!
HUMAIRA!!! kllm zancenka kenan wai da gaske
kai ahaka zaka aureta...?
Faruk yadan tsaya a hankali ya tako tare da
bata rai yace “Eh a hkn ko zaka hana nine??“
Yayi tambayar sanda ya wuce izuwa karshen
falon ya dauko lemon juice da kofi ya juyo
izuwa inda nazir ke zaune yace “idan
munafuncin daya kawoka kenan ka tashi ka
tafi.“
Nazir ya warto kofin da faruk ya dora a dan
karamin tebirin dake gbnsa ya zuke lemon
cknsa yace “haka akeyi? ka gyyceni kuma ka
koreni??
kawai dai nayi mamakin yadda kayi haka anya
baka nuna rashinzuciya ba??“
Faruk ya grgza kai yace “Nazir ba haka bane
ni HUMAIRA bata taba yimin laifi ba, bada
yawunta, sonta ko yardarta abubuwan da suka
faru suka faru ba hasalima jajircewa tayi sai ni
sbd tana da yakini akaina, don haka idan na
juya mata baya yanzu ita nayiwa ba wani ba.“
nazir ya jinjina kai yace “kazo da zance kaima,

ynz dai me kake so ayi??“
Faruk ya gyara zama yace “So nake pls ka sanar da kowa jibi daurin aurena kowa ya shirya ba, nasanka da zafin nama a shirya komai ckn lkc nasan zai yiwu??“
Ah! kwarai me zai hana?? ai ko gobene bazamu kasa kintsawa ba bare jibi.
Faruk ya dago yace “Na sani, zan 2ra maka isassun kudi a account dinka yanzu so nake komai ya kintsu ckn kwana biyu kmr anyi shkr biyu ana shiri, ga mukullin nan (ya jefa masa) na gdna ne nasan kasanshi shima a gyarashi gyara bana wasa ba a shiryashi a kintsashi kada ya rasa komai da ake bukata.“
Nazir ya mike tare da sarawa yace “an gama ‘leader‘ yayi kasa da murya yace “amma dai UMMI fa dole...“
faruk yace “karka damu shawo kanta a guna bame wuya bane kai dai ka zartar da aikinka ka barni da nawa ka hanzarta kaga dare ya taho yi .“
Nazir ya taka kmr zai fita sai kuma ya juyo ya rike baki yace “um!! gskyne gaf kake da kafa record fa saurayin daya zama ango ckn kwana biyu.“
kana gaf da zama MAI GIDA.....
Faruk ya nunashi yace “kai! bana son iskanci, na.... yayi kmr zai bishi.“
Nazir ya kyalkyale da dariya ya fice da sauri.
Faruk ya koma dknsa.
*WASHE GARI da safe faruk ya fito byn ya gama duk abnd zaiyi a falo ya tarar da ita zaune a kujera ya gaisheta ta amsa sama-sama.
Faruk ya gyara zamansa yace “Ummi gameda maganar nan ne ta jiya ina so....“
Kace game da maganar banzan nan ce ta jiya, ta mike tare da juyawa zata bar falon, faruk yayi saurin mikewa ya tsaya a gbnta ya saki hawayensa data fi tsanar gani fiye da komai ya durkushe bisa gwiwoyinsa yace “Don girman Allah ummi ki taimakeni ki fahimceni, kin sani ban isa na aiwatar da komai ba sai da

izininki kuma bazan taba bijirewa umarninki ba domin kece komai nawa.
Ina so nayi wani abu ne guda daya dazai gyara abubuwa da yawa kuma ya samar da alkhairai da yawa, ciki harda ladan taimakon wanda yake bukatar a taimaka masa wanda kin dade kina kwadaitar dani akan haka, kinsha fada min na zama me juriya da yafiya a koda yaushe.
Humaira batayi mana laifin komai ba hasalima keda kanki yabonta kike kuma itama bata so akai mana haka ba idan na gujeta a yanzu ba wani nayiwa ba ita nayiwa, na tbbtr idan na barta zata shiga kangi da takura fiye da ko yaushe a rywrta nasan kuma kema ba zaki so a gujeni don wata kaddara ta fada min ba!!“
Jin tayi shiru yasa ya kara tausasa lafazi yace “2n ba yanzu ba kin dade kina fada min yadda karshen rayuwar masu HALACCI, CIKA ALKAWARI da RIKE AMANA take yin kyau ki taimakeni na zama daya daga cksu don Allah.“
Ta bishi da kll da alama kalamansa sun ratsata ma2ka, da dawo da baya izuwa kan kujerar jim kadan tace “kai yanzu wane shiri kayi??
Shirina bame wuya bane umarninki kawai nake jira.
Ina ka shirya kaita to byn auren??
Ta sake tambayarsa.
Ya bata amsa da fadin “Gidan da kika fada min cewa shima nawa ne dana gada a wurin mahaifina kuma kika bani mukullinsa da komai nashi da hnnki can zan kata mu zauna idan kin amince.“
Shikenan ya zanyi da yin Allah?? Na amince Allah yasa hkn shi yafi alkhairi.
Fuskar faruk tayi gaggawar washewa yayi saurin mikewa ya dawo gbnta ya zauna tare da cewa “Abinda nake so ki fada kenan ummi nasan kuma zaki amince shi yasa nake godewa Allah daya bani ke NA GODE sosai ummina, amma kina ganin su kawu zasu amince kuwa??“

Ba dole ba??
Tayi saurin fada.
Kaifa maraya ne kowa so yake yayi maka abnd zaisa kayi farin ciki ko don ya sami lada ka bari zamuyi magana dasu kaje kawai.
ckn farin ciki faruk ya fita daga gdn.
Hakika abnd Allah ya kadarta faruwarsa babu abinda ko wanda ya isa ya dakatar dashi.
Da ana SO da ba'a SO, Ana kuka ko ana dariya, dole aka daura aurena da faruk a ranar da lokacin a kuma inda aka shirya.
Ranar da bazan manta da ita ba a rayuwata, daga waje biki yayi armashi ma2ka sbd ba wanda yasan halin da ake ciki, kai ko a gdn wadanda ya zama dole su sani ne kawai suka sani.
A gdnmu kam naira jknta ya gaya mata, daddy masu sakin famfon kudi haka kawai ma bare da dalili.
Kowa yayi mamakin faruk da irin abubuwan da yayi a sannan ne daddy ya tbbtr faruk ba irin talakan da yake tsammani bane!!
Washe gari byn komai ya lafa dare nayi aka kaini gdn faruk, gdn sabuwar rayuwa, gdn farin ciki, gdn jin dadi da walwala.
Ba wasu mutane masu yawa bane suka rakoni hakan yasa ba jimawa kuwa kowa ya watse ya zamana daga ni sai MUFIDA, ina zaune bisa shimfideden gadon da a yanzu nake jinshi fiye dana sarauta ma daya zarce na alfarma.
Mufida na zaune sai zuba take ta inda ta shiga ba tanan take fita ba, da yake uztaziyya ce a nasihar tata harda ayoyi da hadisai, maganganun nata na ckn ratsani naji tayi shiru jim kadan ta mike tare da jawo mayafinta da jakarta zata fice, nayi gaggawar dago kai na damko hannunta wasu hawaye sukayi saurin gangaro min nace “MUFIDA kema tafiya zakiyi ki barni ni kadai??“
Ta bini da kallo tausayina ya bayyana karara fuskarta, ta dawo ta zauna gaf dani tace “dole zan tafi sbd nan gdnki ne ba namu ba, gasu can a waje ni kadai suke jira mu tafi FARUK

yananan tafe KIYI HAKURI.“
Ta banbare hannunta daga nawa ta fice tana waigena.
Daga nan sai naji ni a wani irin yanayi, ba wanda zai zauna??
Wace irin rayuwa na shigo kenan??
Kodai basa sona shi yasa kowa ya tafi??
Tunanin da yayi ta yawo a zcyt a wancan lokacin..!
Hmm da kina tunanin xasutayaki xamane...
Koya wannnan zaman aure zekasance..? Se ku biyoni INSHA ALLAH..!
Ina nan zaune ni kadai bisa tsakiyar makeken gadon da nake kai, jikina na sanye da kaya na alfarma kaina na kasa kirjina na dukan uku-uku na rashin sabo.
Sallamarsa da naji tasa naji wata nutsuwa tazo min sautin muryar tasa ya daki kunnuwana kai tsaye ya fara zagaye a kwakwalwata, ban dago kai ba shi kuma baiyi magana ba ya zauna ta salo na fuskantar juna ya kura min ido kawai.
Na dan dago kai a hankali na dubeshi nayi saurin mayar da kaina, yayi murmushi tare da cewa “yes dago mana ya kika fasa my AMARYA!!
kodai tsorona kike ji??
Na girgiza kai nace “Koda ace za‘a wayi gari kowa ya zama abin tsoro a gareni na tbbt banda kai.“
To ki dago kanki.
Na yace mayafin dake kaina tare da dago kai fuskata wadda hawaye ya gama jikata sharkaf ta bayyana.
FARUK yadan yi baya da kansa kmr yaga abin tsoro yace “Kuka kuma?? Maimakon murna da farin ciki??“
Na girgiza kai ckn sheshsheka nace “ni nafi cncnta nayi kuka fiye da kowa, mafi yawan amare nayin kuka amma na munafunci ne ni kuwa nawa kukan na dolene sbd rayuwa bata zo mana a yadda yakamata ba, laifin me mukaiwa duniya da tayi mana wannan horon

FARUK...??
ya kauda kansa tare da cewa “ki daina fadan haka HUMAIRA ba muka iya da yadda Allah ya kaddara, Ai dai gamu a tare matsayin MA‘AURATA wannan shine bbn abu mafi jin dadi daya kamata ki rinka 2nawa. Na kara kasa da murya nace “ma‘auratane mu amma ba kmr saura ba 2nda mu muna da nakasu ta bangarori da yawa kowacce amarya takan zauna ne a tankwashe amma ni kafuna kaga a mike suke daga sama har kasa ba wani motsi da zasu iya yi, kaga kenan ni nakasashshiya ba wani amfani da zanyi a garek......“
Yadan zaro min ido tare da katseni yace “HUMAIRA!!“. yabini da kallo ya dora da fadin “don Allah ki daina fadar haka, idan baki manta ba a baya na taba sanar dake cewa ba ina sonki ne don bukatuwar samun wani abu daga gareki ba, ina sonki ne a mtsynki na humaira gnnki a kusa dani kawai ya wadatar dani.
Kuma ai larurarki ta iya wani lkc ce ba‘a ce ta har abada ba don haka zaki warke kuma muyi rywa kmr sauran MA‘AURATA.
Tarayyarmu bata wani dan lkc kankani bace ta har abada ce, babu wani dalili dazai rabamu har abada.
Ki rinka 2na wannan a koda yaushe.“
Ckn sheshsheka nace “a baya na dade ina hango yadda rayuwar aurenmu zata kasance ckn farin ciki walwala da jin dadi sai gashi tazo mana akasin haka, tazo da babban nakasu.“
faruk yace “ki daina kawowa zamanmu babu farin ciki sbd kawai kina da larura, duk inda HUMAIRA da FARUK suka kasance tare akwai tbbcin farin ciki a wajen a kowanne irin yanayi ne.“
nadan bishi da kallo nace “Me yasa ka hana a bamu y‘ar aiki da zata taimaka mana, alhalin sanin kanka ne ba abnd zan iya yi.
Yayi saurin girgiza kai yace “babu bukatar wani ya shigo ckn rayuwarmu ya taimaka

mana mu zamu taimaki rayuwarmu da kanmu
kuma mu tafiyar da ita yadda muke so, zamuyi
zama irin wanda ba‘a taba yin irinsa ba.
Na tbbt Allah daya haliccemu zai taimakemu.“
“girki, goge-goge, share-share, wanke-wanke
duk waye zaiyi wadannan ayyukan??
Na tambaya ina dubansa.
ya mayar min da amsa da cewa “duk nine.“
Idanuna sukayi saurin tafiya yawo sbd
AL‘AJABI!!!!!
kai kuma??
Naka aikin kuma fa ko shikenan a gida
zakayita zama??
“A‘A! aikina yana nan amma bazai shafi
wannan ba.“ Wasu sababbin hawaye FIL suka
sulalo min.
Lallai bana jin za‘a samu mu2m irinka duk
duniya!! ka sarayar da hakkinka da duk wani
ango ke buri idan yayi aure sannan ka dauki
alhakin aiki mafi girma akanka duk sbd ni.
Ina rokon Allah ya kawo sababin da nima zan
nuna maka HALACCIN da kayimin duk da
nasan zaiyi wuya nayi maka irin abnd kayi min
sai dai na kwatanta.“ Na kwantar da kaina
bisa cinyoyinsa na fashe da kuka.
Mun dau tsawon lkc a haka dakyar faruk ya
rarrashe ni na iya yin shiru, da kansa ya tashi
ya zubo min abnc ya tilasta min sai da naci
sosai.
Ya dauke plask din da sauran kayan ya mayar
dasu wajensu ya tako a hankali yace “To kinga
yanzu lkcn kuka ya wuce ki kwanta kiyi barci
isashshe kada kiji komai a gdn masoyinki
FARUK kike..
yakai karshen maganar dai-dai sanda ya
zauna a dan karamin tebirin dake gefen gadon,
nabishi da kallo har yanzu hawayen idona
basu kafe ba saima kara gudu da sukeyi.
Na dubeshi nace “amma wannan rana tazo
mana ba yadda yakamata tazo ba, me yasa
ma haka zata faru??...“
Faruk ya dan kauda kai ya dawo ya dubeni
yace “ki bari!! zakiyi sabo fa! idan kika ce me

yasa, kai tsaye Allah kenan fa kike tambaya.
Haka Allah ya kadarta mana koda a haka zamu tafi har mu2wa ni bani da kaico, kada ki karya zuciyarki da yawa duk wanda yasanki yasanki akan dakakkiyar zuciya me zai hana ki dawo ki cgb da zama a haka??“
Na girgiza kaina nace “zaiyi wuya koda zai yiwu badai a ynz ba.“
Ya bini da dogon kll yadan zunburo baki yace “Zamu bata idan baki daina kuka ba.“
Na goge hawayen idanuna.
Yace “yauwa ko kefa??
Sai ki kwanta kiyi barci ki samu isashshen hutu kinji??
Na gyada kai kawai nabi gadon na kwanta nace “kai kuma ina zaka??“
Zanyo alwala nazo nayita sallah na godiya ga ubangijina daya bani ke.
Zan bika muyi tare.
Na fada ina dubansa.
Ya girgiza kai yace “A‘A my amarya aike kina da lalura barci shine mafi dacewa a gareki a yanzu.“
Ka daina kirana da amarya sbd lalura ta hana na amsa wannan sunan, ban kuma san sanda zata barni na warke harna amsa sunan ba.
Na fada.
Yayi saurin cewa “manta da wannan“ ya jawo bargo ya lullubeni har zuwa wuyana yace “kiyi nutsatstsen barci da safe zaki fada min kalar mafarkin da kikai.“
Yakai maganar murmushi na tashi daga fskrsa, fuskata ta fadada da murmushi nima na gyada kai kawai.
Ya juya ya dauro alwala akan idona ya fara sallah sautin kara2n da yake yi yana ratsa kunnuwana har barci ya kwashe ni.
*WASHE GARI da asuba faruk ya tasheni nayi sallah a zaune kmr yadda na saba yi barci na koma sbd akwai shi a idona sosai.
Misalin 8:15 na safe faruk ya tasheni a karo na biyu, cak ya daukeni ya dôrani bisa kekena ya seta kafafuna a matokarar keken dake kasa

ya 2rani a hankali muna hira kai tsaye muka fito falo ya wuce dani gefe falon inda aka tanadi wani faffadan tebirin cin abinci zagaye kujeru ya 2rani har izuwa gbn kayataccen tebirin ina zaune bisa keken da aka halitta sbd irinmu.
faruk yace “yauwa kinga ke y‘ar baiwa ce ba ruwanki da kujera, ni kuwa bin tebirin kawai nake da kll zagaye yake da abinci kala-kala irinna breakfast kuma dafawar yanzu sai tiriri suke kana gani kasan yanzu aka hada su.
ckn AL‘AJABI nace “waye ya dafa duk wannan abubuwan??“
Yayi murmushi yace “Nine!! kina mamakine??“
Ya fada dai-dai sanda ya ajiye kofin tea a gefena tare da cewa “bismillah! sai ki fara da duk wanda kike so.“
A ido kawai nasan duk abinda ya dafa zasuyi dadi ma2ka sanda nakai bakina dazan hadiye har wani lumshe ido nayi, na bishi da kll nace “a jami‘o‘in koyon girki wacce kayi??“
Yayi dariya yace “A jami‘ar ummina mana, 2n ina yaro tare muke yin komai gashi kuma yanzu hakan ya fara amfani.“
Haka dai muka cgb da cin abincin ckn nishadi muna hira har muka gama, faruk ya fara shiga dani loko da sakon na gidan.
*Haka dai muka cgb da rayuwa har hu2n faruk ya kare ya koma wajen aiki sai ya zamana kafin ya tafi duk abinda zan bukata ya aje minshi bisa faffadan tebirin dake gaf da makeken gadona.
Abinci, ruwa, magungunana da komai suna kusa dani sai kuma uwa-uba wayata wadda da ita muke tare a ko yaushe.
kllm sai ya dawo ya koma, da la‘asar tayi kuma ya dawo gida ya shiga kitchen da kansa ya dafa mana abinci.
A wasu lktn tare muke shiga ina zaune bisa dan kekena muna hira har mu gama hada abnd muke so, rayuwarmu abin sha‘awa ckn sauki muke gudanar da ita cike da walwala da aminci wanda hakan ya samu ne ta silar

tsantsar SOYAYYA ta gsky.
Anya kuwa...za daure..
A wasu lktn idan na dubi a yadda rayuwarmu ke tafiya sai naga kmr a mafarki don ban taba zaton zan tsinci kaina a hali kwatankwacin haka ba, da ace shekaru biyu kacal da suka wuce wani zai fada min cewa haka zata faru koda zai nutse a kasa don rantsuwa bzn yarda ba.
Amma gashi na tsinci kaina a wata irin rayuwa daba haka nayi zato ba, sai dai ko ba komai wasu darussa ne na koya na rayuwa da bazasu taba gushewa daga kwakwalwata ba.
*da yake zancen duniya baya buya a ckn dan kankanin lkc maganganu suka fara zagaye gari, nan fa kasuwar gulma da tsegumi ta bude masu mamaki da rike baki nayi masu salati da sallallami nayi, masu jinjinawa faruk nayi masu tausaya masa nayi.
A fahimtar wasu kuskure ya tafka babba dazaiyi dana sani a gaba, wasu kuma na kllnsa wanda kuruciya tayiwa yawa.
Amma ko kadan bai kula da hkn ba saima kwarin gwuiwa da yake kara samu na kyautata min da nuna min soyayya iyakar iyawarsa, hkn yaba mutane mamaki ma2ka da gaske. Wato ni kaina idan na kalli faruk ina mamakinsa musamman yanzu dana kara kusanta dashi banyi kuskure ba idan nace ba kmr kowa yake ba tbbs shi daban ne wanda samun mu2m kmrsa zaiyi wuya.
A kwana a tashi kwanaki sai kara garawa suke zaman mu na kara daukan lkc, syy da kulawa, kauna da shakuwa na daduwa.
Mu kadai muke gudanar da rayuwarmu kmr yadda faruk yace haka yake so mu kasance, ko ziyara ba wanda ke kawo mana harta da momina sai dai kawai muna yin waya wasu lktn, ba'a zancen daddy dama amma banga laifinsu ba da wane ido zasu kll faruk??
Wanda suka batawa da mummunan sharri ya saka musu da mafi kyawun alkhairi.
hmmm... Abin da kunya ai.

**kmr kllm yauma zaune nake bisa gadona na kishingida misalin karfe 4:45 na yammaci tsammanin dawowar faruk kawai nake nama yi mamakin yadda yau bai dawo da wuri ba don mafi yawa ana kiran sallar la'asar yake dawowa, a hakan har barci ya kwasheni.
ban jima da tafiya nahiyar baccin ba faruk ya shigo da sllmrsa yayi shiru sanda ya tbbtr ba yadda zanyi na amsa don bansan yana yi ba.
ya dan tsaya ya bini da kallo kawai murmushi ya tashi daga fuskarsa ya rankwafo tare da sumbatar goshina ya dago yace "ohh!! my lovely wife Allah ya kara miki lfy."
bai tasheni ba Ya juya ya wuce izuwa bathroom.
Byn wasu y'an min2na na farka, na dubi agogo 5:05 lallai yau faruk ya dade bai dawo ba na fada a zuciyata, ta yiwu wani muhimmin abu ne ya tsayar dashi.
Nayi saurin bawa kaina tbbs akan haka domin bisa al'ada baya kaiwa haka don wasu lktn ma ana kiran la'asar yake shigowa.
Kmr na kirashi sai kuma na fasa, da yake da wata kishirwa na farka matsowa nayi bakin gadon na jawo ruwan SWAN dake ajiye bisa dogon tebirin dake gefen gadon gaf da fuskar gadon wanda ke dauke da abubuwa da yawa.
Irin daukowar gaggawar da na yiwa robar ruwan yasa ta subuce ta fadi kasa tare da gangarawa nesa sosai da gadon, gashi ina bukatar ruwa sosai hakan yasa na matso bakin gadon tare da kwantawa na mika hannuna don dauko robar, sai dai ina!! hannuna ya gaza kaiwa inda take.
Nayi iya kokarina na mika hannuna iyakar mikawa amma ya gaza kaiwa, 2nanin dana fara yi shine wai yau nice ga abu ina so amma na gaza iya daukarsa kuma ba wanda zai bani.
Musamman idan na 2na rywr baya yadda zan hantara inyi tsawa a aikata min koda ba'a so sai gashi yau wanda zan yiwa magiya yayi min ma babu shi a kusa.

Nayi wani spring ta gefe na koma zaune hawaye wadanda suka zama sabo na suka gangaro min, na zuba tagumi na rasa abnd kemin dadi a duniya.
Dai-dai Ikcn ne FARUK ya dawo daga inda ya shiga izuwa dakin fuskarsa tayi saurin canjawa ya bini da kallo, jimawa kadan yace "HUMAIRA!!"
firgigit nayi kmr wadda ta farka daga barci muka hada ido, kll daya nayi masa nasan ba yanzu ya dawo ba nayi saurin goge idanuna nace "Uhum!! dama ka dawo??"
Lfy?? meye ya faru kuma??
ya tambaya yana dubana.
na girgiza kai nace
"uhm..uhm ba komai meka gani??"
Ya tako a hankali yace "koda banga hawaye a idonki ba kll daya zanyi miki nasan da wani abu, abin mamakin min2na 15 da suka wuce ma dana shigo barci kike yi ko kinyi wani mummunan mafarki ne??"
Na girgiza kai alamar a'a.
Ko don ban dawo da wuri ba??
Sake tambaya yana dubana.
Nayi saurin sake girgiza kai a karo na biyu.
ya bini da kll da fadin "meye ya faru to??".
na dan kauda kaina a hankali nace "ba komai."
na fada idona nakan robar ruwan data fadi 2n dazu, faruk yabi inda idona yake da kll idonsa yakai ga inda take ya kalleni ya kalli robar tare da takawa ya daukota, ya dawo inda nake da fadin "mu2m najin kishirwa yana ganin ruwa ya gaza samu abin da ciwo kam.
Ya zauna a tebirin dake gaf da gadon muka yadda zamu fuskanci juna sosai ya juya ya dauko kofi ya tsiyaya min ruwan tare da miko min, ba gardama kuwa na amsa tare dakai kofin bakina na zuke ruwan.
yace "abinda yasa ya fada kasa wai yanayi miki nuni da cewa na shigo ne, wanda yakamata ya baki da hannunsa ya shigo don me zaki wahalar da kanki don Allah ki bari faruk ya baki da hannunsa. abinda naji robar

na fada kenan yanzu dana daukota.
Duk da gun2n hawayen dake idona saida nayi murmushi har dariya ta kwace min.
hmm... me kwantar da hankali yayinda ya tashi kenan.
Ya gyara zama yace “idan kina kuka ko sai in rinka ganin kamar ba humairar dana sani a baya bace, HUMAIRA y‘ar kwalisa me jin kai da girma da martaba komai nata da isa take yinsa, ga taurin zuciya da juriya komai na kasaita ne.
Bata taba karaya bare har tayi kuka hawayenta su zuba, me yasa kika canja????
Na bishi da kll kawai nace “rayuwa ce ta canja ni sbd naga abubuwan AL‘JABI masu yawa da suka koya min darasi a rayuwa wanda indai zan rinka 2nasu hawayena ba zasu daina zuba ba har abada.“
Zasu daina mana.
Ya fada tare da cewa “Dole sai kin manta abinda ya wuce zaki samu nutsuwar fuskantar abnd zai zo a gaba, kefa daban ce kuma babba ce, mahaifinki babban dan kasuwa me arziki ma2ka, ke kuma kina da baiwar ilmi, fahimta da alfarma me yawa.
Na kada kai nace “OK na zaci girman ta bangaren hikima, hazaka, tausayi, alkawari da amana kake nufi dasai ince sai dai kai!!
Domin kai sai bayan shekaru ashirin ake sake haihuwar irinka a duniya.(hmm anya kuwa koni abdool aina fishi.)
Ya dan daga gira kadan tare da mikewa yadan taka, nace “ina zuwa??“
Ya juyo tare da cewa “zan shiga kitchen baki ga nayi dress din girki.“
nabi y‘ar karamar rigar dake jknsa da kll hade da wando wanda da kadan ya wuce gwiwa, irin kayan nan ne masu yanayin jersey da basu da nauyi sai P-CAP dake sanye akansa 2n daga sama har kasa duk launin yellow ne dasu nayi murmushi nace “To a fito lfy amma ka tbbtr ka kula da wuka sbd tana da kaifi, snn ka kula da wuta sbd tana da zafi.“

Ke kuma ki kula da ruwanki sbd kada ya kara fadowa. Ya fada tare da juyawa.
Nabishi da kll kawai nadan kada kaina dariya ta kwace min.
Ya yaje bakin kofa sai kuma ya juyo tare da takowa yace “my queen me kike sha‘awar ci ne yau??“
kmr bazan ce komai ba sai kuma nace “Fried rice idan ka iya.“
Yadan kara takowa a hankali tare da maimaitawa “fried rice! fried rice!! kai gsky.....“
Rabu dashi kawai kayi koma meye.
Nayi saurin fada. Ya girgiza kai tare da cewa “ba za‘ai haka ba 2nda shi kike so to sai mun cishi yau, abnd za‘ai ba dake zamu je kitchen idan ni ban iya ai ke kin iya, sai zama director kina zaune a kekenki na sarauta kina bada umarni.
Daga yau kinga nima sai na kara ilmi ko??
Ya karasa fada sanda ya karasa inda kekena yake ya 2roshi dai-dai bakin gadon.
Haka kuwa akai a hankali ya 2rani bisa keken izuwa kitchen muka fara aiki.
Ina daga zaune ina yi masa nunin abubuwan dazai hada don yin fried rice ckn nutsuwa, idan bai gane bama 2rani yake har inda abin yake nayishi da kaina. A haka har muka gama hadawa tare muka dawo izuwa falonmu.
Irin wannan shine taimakon kanmu da kanmu da mukeyi kuma muyiwa kanmu komai ba wanda yakeyi mana.
Kwanaki nata zuwa suna shudewa sannu a hankali, kulawa daga faruk babu alamun raguwa saima karuwa a koda yaushe.
**BAYAN SHEKARA DAYA**
zai yiwu bazai yiwu ba, zamu jure ba zamu jure ba, zai iya faruwa ko bazai iya ba da wasu keta cece-kuce duk sai yazo ba yadda da yawan mutane suka zata ba.
sai da muka shafe tsawon shekara daya cif a haka yadda muke.
Abin sha‘awar babu korafi ko canjin yanayi a tare damu sai ma karin karfin gwiwa da muke

samu da kuma tbbs soyayyarmu da tbbs na rayuwa tare har abada.
Wato mun riga mun zama daya na zama faruk ya zama ni domin idan na fahimta dai-dai ko a fuska kamanninmu sun juye sun zama daya.
dangane da larura ta A kllm jina nake akwai alamar sauki a tattare dani sai dai bana yarda da hakan, a yanzu ina jin cewa akwai kafafu a jikina sabanin baya.
A kllm kuma sai nake jin suna kara karfi har nakanyi 2nanin me zai hana na gwada mikewa amma idan na 2no da gargadin likita acan baya sai na hakura.
Abinda na tbbtr shine akwai ranar da zata zo zan mike na tafi akan kafata don na dade da fara jin alamun haka.
*Kamar kllm yadda ya saba fita misalin karfe 10:00 na safe ina zaune bisa kekena faruk na tsaye jakarsa na hannuna ya gama shirinsa tsaf zai fita na bishi da kll nace “you look very fresh my life, amma zaman hularka da gyara.
Ya tsugunno dai-dai da fuskata tare da cewa “gyara min dai-dai da yadda kike so.“
Na cire hular a hankali tare da gyara karinta na mayar kansa tare da daidaita zamanta naja hannuna baya tare da lankwasa dan yatsana alamar jinjina.
Ya mike na mika masa jakarsa da fadin “fatan alkhari, sa‘a, da nasara a gareka mijina.“
Ya karba tare daja da baya yana kllna yace “ameen matata, zadai ki iya tuka kanki ki koma daki ko???“
Na gyada kai nace “Eh kasan ai keken na zamani ne wanda yake kaima zai iya sarrafashi nayi sa‘a ni gurguwar zamani ce bata daa ba.“
Kidai bi a hankali kinsan KARFEN NASARA....“ Ya fada yana me nuno ni da dan yatsa.
Nayi dariya nace “nafa yi karfi yanzu nayi kwari sosai don ni a yanzu ji nake kmr ma zan iya mikewa nayi tfy da kafata.“
FARUK ya girgiza kai yace “habawa!! da saura kada ma kice zaki jaraba don bazai yiwu ba,

ko kuma kima gwada 2n yanzu a gabana don ki tbbtr bazaki iya ba kada ma in tafi ki gwada hakan.“
Na bishi da kll nace “kaban izinin hakan??“
Ya gyada kai tare da matsowa wai kozan fadi ya taroni.
Na jinjina kai nadan runtse idona tare da yin bismilla na yunkura a karo na farko na tashi tsaye, ni kaina bude idona kawai nayi na ganni a tsaye kyam!!
Kmr daga sama lkc guda naji karfi ya shiga ckn kafafuna ko don dama rashin motsasu na sawa bana jin karfinsu??
Nan fa fuskar faruk ta fara canjawa yana kllna kawai ckn mamaki.
Ni kuwa kawai sai na motsa na daga kafata tare dayin tafiya nayi taku uku akan kasa sannan ne tbbtr da abinda nake zato, tbbs kafafuna sun dade da dawowa dai-dai nice kawai ban sani ba.
Sbd AL‘AJABI idanun faruk zarowa sukayi waje kamar zasu fado sai kllna da yake yi ya kasa magana, na dubeshi nace “faruk na warke fa.“
Kara takawa mu gani!!
Na daga kafata na taka nayi tfyr dani kaina banyi zato ba naji ni damurmur akan kasa ko alamar layi banayi bare na fadi, jina nayi a yanzu tamkar ban taba samun wata matsala ba.
Faruk yayi wurgi da jakar hnnsa izuwa kan kujera ya tako izuwa gabana a hnkl bakinsa ya furta sunana “HUMAIRA!!!“
muka rungume juna sbd farin ciki da murna, wasu sanyayan hawaye suka gangaro bisa kuma2na.
muka fuskanci juna sautin dariyar farin cknmu me hade da hawaye ta fara tashi, faruk ya goge hawayen kuma2na da hannunsa ya girgiza kai yace “ba lkcn kuka ne yanzu ba, asibiti zamu tafi yanzu don mu sami tbbs daga bakin doctor shirya maza.
Faruk har wata y‘ar karamar rudewa yayi,

kayan jikinsa ma canjasu yayi yasa wasu.
Muna fitowa motarsa muka hau wanda ke kula da gate din gdn ne yake jan motar sbd murna ba zata barshi yayi 2ki ba, da mun hada ido murmushi ke tashi daga fuskokinmu.
Ban taba tsintar kaina a farin ciki kmr na yau ba, sai da takai magana ma bama yiwa junanmu sai murmushi sai dariya har muka iso makeken asibitin da shekara daya kenan rabona dashi.
Duk inda na kalla a cknsa baya nake 2nowa. salih Ka dan jiramu zamu fito bada jimawa ba, faruk ya fadawa wanda ya jawo motar.
To ranka ya dade.
Salih ya fada ckn ladabi.
Muka juya izuwa ckn asibitin kai tsaye.
******* ***********
Shekara daya kenan banga wajennan ba, duk inda na baya kawai nake 2nawa sanda aka kawoni magashiyan na rikito daga bene yau kuma gani na dawo da kafata. kai tsaye bangaren da aka kwantar dani shekara daya data wuce sanda larura ta sameni muka wuce, muna isa kuwa aka taremu nan fa wasu likitoci mata su biyu suka sani a daki aka fara gwaje-gwaje da aune-aunen kafata 2n daga sama har kasa, na jima kafin daga bisani su kammala.
babban lktn ya umarcemu muje ofis dinsa mu jirashi, haka kuwa akai muka shiga ofis din tare da zama a kujeru biyun dake fuskantarr ta kujerar likitan.
Addu‘o‘i kawai nake mai-maitawa a raina Allah yasa karshen matsalarmu yazo gaba daya, Allah yasa muji tbbcin komai ya dai-daita kmr yadda muke da yakini.
Bayan tsawon lkcn da muka kwashe a zaune likitan ya shigo da saurinsa tare da yi mana sallama, muka amsa faruk ya mike suka gaisa ckn girmamawa suka zauna a tare.
Likitan ya dubemu tare dayin murmushi yace “FARUK*HUMAIRA ko??“
muka gyada kai kawai mudai abnd ya kawo

mu kawai muke son ji.
ya kada kai tare da zaro wata sabuwar takarda daga gaban aljihunsa ya dubemu ya sake yin murmushi yace “humaira sannu fa, kinsha wahala amma gskyr hausawa da suka ce komai yai farko zaiyi karshe, Allah me magani.“
Muka dubi juna fuskarmu tadan kara saki.
Likitan ya gyara zama ya mayar da idanunsa ga faruk yace “a baya kmr yadda mukayi maganar da mahaifinta akan lalurar data sameta idan ban manta ba na sanar dashi cewa matsalar data samu bata din-din-din bace lkc zaizo da zata warke kwata-kwata sai dai babu yakinin ko yaushe ne.
Ah wato duk yadda nake da yakini akan cewa zata warke amma ban taba 2nanin abune da zaizo da sauki koda wuri ba.
Yadan dakata tare da rike baki kadan yace “Abin ya bani mamaki da AL‘AJABI ma2ka da gaske ni kaina ban taba 2nanin zata warke a dan kankanin lkc haka ba, Allah ya nuna ikonsa!!
Ina me tayaku murnar kin warke babu wani kafarki ta dawo kamar ta kowa kina da damar takata zuwa duk inda kike so ba wani sauran ciwo a tare da ita.
Mukayi gaggawar duban juna nida faruk ido cikin ido a hankali murmushi ya fadada a fuskokinmu, faruk ya matso gaban kujerar da yake kai tare da fadin “ina me bakin cikin kasa yi maka komai a matsayinka na wanda ya bani albishir mafi dadi a rayuwata, hakika da ace ni me tarin dukiya ne da kudi yau sai ka gaji da cewa a barsu haka, sai na cika maka harabar gdnka da motoci, na gina maka manyan gdje na gani na fada, kana duk shekara sai kaje aikin hajji da umara.
Doctor yayi dariya tare da cewa “faruk kenan da abin dariya kake, yin Allah kenan a kiyasce shekara biyu na daukarwa al‘amarinnan gashi Allah yayi ckn shekara daya kacal.“
yakai karshen maganar yana dubanmu.

Faruk ya dubeni mukayi farr da ido a tare muka zarce da yalwataccen murmushi tamkar zamu 2ntsire da dariya.
Mun dade munayi masa godiya kafin mu fito.
Tare muka jero muna fitowa na ciro wayata na fara kiran mufida na sanar mata, jinta kawai nayi amma nasan bata taba farin ckn da tayi yau ba.
Muka karasa jkn mota faruk ya dubeni yace “hmm... lallai kina ji da kawarki irin wannan lbrn ba‘a fara sanar da momi ko daddy ba sai ita???
suma duk zasu ji ai lambarta ce ta fara zuwar min a farko.
Na fada kawai amma a zuciyata nasan dalili, mufida tayi min halacci duk abnd ya faru baisa ta watsar dani ba tafi kowa kula dani idan ka cire faruk.
Tsayar da dan tasi din da faruk yayi ne ya bani mamaki nace “a mota muka zo fa koka manta??“
Ya grgz kai yace “Ina sane kuje gd a wannan motar zan tafi a tasin nan zuwa wajen aiki akwai wani documents da suke nema ni kadai nasan inda yake kinga sun yimin text yafi guda ashirin.
Amma faruk....
Ya katseni da fadin “karki damu!! ko awa daya bazan kai ba na dawo gdn, ya juya ga salih yace “ku koma gd nima ina tafe, amma wlh kabi min sarauniyata a hankali.
salih yayi murmushi kawai ya amsa da TO.
Bari nayi sauri inje ko??
Ya fada.
Na gyada kai kawai na bishi da kallo har yayi gaba sai kuma ya dawo ganin kallon da nake masa.
Yadai?? menene??
Ya tambaya.
Na dan gîrgiza kai nace “ba komai.“
Nayi saurin fada.
To jeki ku tafi sai nazo.
Ya juya ya shige tasin suka tafi nayi ta kallon

motar har sai data bace min.

Na juya na shiga motar da muka zo da ita salih ya juyata muka bar wajen.

Wani iri naji da faruk ya fadi zai je inda ya tafi, amma ai na saba jin haka duk sanda zamu rabu da faruk.

hakan yasa na share kawai.

Bayan mun iso gd ina isowa dan karamin falonmu wani tsallen farin ciki nayi na fada kan kujera.

(akwai masu cewa basuga wani part ba da mukawuce me buqata se ya shiga wannan pagedin(y) ßADI ßA RAI.
dan samu complete)

Rayuwa sabuwa yau akwai shagali, dawowar faruk kawai nake jira.

Na tashi na shiga nan na fita nan nayi ta kewaya gidan sai yanzu na kara gane gdn, da yawa sai yanzu naga wasu abubuwan.

Na shiga bathroom nayi wanka na fito na caba kwalliya irin wadda na manta rabo na da nayi irinta, jina nake kawai na dawo wata sabuwa.

Na wuce kitchen kuma na shirya hadadden girki na dawo falo na zauna na kurawa wani hotonmu nida faruk ido wanda aka hadashi mun yi kyau sosai.

Ina nan zaune Bayan akalla min2na talatin wayata tadau ringing na dagota nayi arba da faruk nayi murmushi nace DAN HALAK ina ambatonka a raina kana kirana a waya, na daga nakaita kunnena fuskata cike da annuri.

Na karasa kai wayar kunnena yalwataccen murmushi na tashi daga fuskata, sai dai tayi saurin canjawa daga annuri zuwa rashin fahimta sanda naji muryar dana tbbtr ba tashi bace.

..inna lillahi wa'inna ilaihirraji'un..nafada..
Kome ke faruwa..!

Na karasa kai wayar kunnena yalwataccen murmushi na tashi daga fuskata, sai dai tayi saurin canjawa daga annuri zuwa rashin fahimta sanda naji muryar dana tbbtr ba tashi bace.

Idan har a yadda muka fahimta dai-daine Ga
alama kece matar me wayar nan ko??
Ckn y'an sakannin da yayi na maganar 2n
kafin yakai karshe fuskata ta rikide daga yadda
take a baya zuwa mummunan yanayin daya
wuce misaltawa nayi saurin cewa "Eh...eh nice
la..fiya meye ya faru??"
ka2war muryar tamkar ana buga diro dake
magana tayi shiru zuwa can tace "To kiyi
gaggawar zuwa asibitin SABO TAIWO
HOSPITAL mijinki ya samu mummunan
accident..."
Iya abnd kunnuwana suka iya jiye min kenan
suka dauke dif ma'ana suka daina jin komai,
wani duhu ya ziyarci idanuna na daina ganin
inda nake tsaye ma bare nesa. Kaina kuwa
wata irin juyawa ya fara yi kwatankwacin
yadda belt din inji ke juyawa sanda yake aiki,
wani gumi me zafi ya fara ketowa ta ko'ina
daga jikina tamkar an watsa min ruwan zafi.
(wani yasaman yacemin wai ina tsalleke..to ni
ban tsallake duk wanda be gani haq qarke to
se ya koma ta opera zegani har inda mu ka
tsaya..)A tsaye nake na kasa gaba na kasa
baya, a takaice dai gaba daya na dauke wuta,
ni kaina banyi yunkurin motsawa ba don nasan
faduwa ce zata biyo baya saima mika hannuna
da nake yi wai ko zanji bango na dafa amma
babu. Na shiga yanayi mafi muni 2nda uwata
ta haifeni yau sanadin MUMMUNAN ALBISHIR!!
Bansan sanda wayar ma dake hannuna ta
subuce zuwa kasa ba, tana dira kuwa ta
tarwatse komai nata ya rabu da dan uwansa,
na dade a tsaye tamkar gunki dafe da kaina
dake juyawa.
Zuwa jimawa kadan dana ji dan dama-dama
na yunkura da karfi daga inda nake tsaye wani
jiri ya kwasheni ta gefe nayi kasa sai dai bisa
sa'a jina kawai na fado akan kujera, na
dunkule kaina na fashe da kuka hawaye na
zuba tamkar ruwan sama.
Zaiyi wuya in ban rasa faruk ba. 2nanin da
nayi kenan wanda yasa nayi gaggawar mikewa

duk da ban gama dawowa dai-dai ba na jawo mayafina, takalmina da mukullin motar faruk duk na rikesu a hannuna nayo waje da gudu. Banma yi yunkurin tsaida kukan da nakeyi ba don nasan bame yiwuwar tsayawa bane.
ganin a yanayin dana fito yasa salih tasowa tare da tambayar "hajiya Ify??
ya na ganki haka??
me ya faru kike kuka kuma??
Na daga baki dakyar nace "Faruk ne.. sunyi accident yanzu haka suna...asibiti..."
Nakai karshen maganar dakyar.
Subhanallahi!! Accident??
shima ya fada a gigice, hankalinsa ya tashi ma2ka.
Yayi saurin amsar mukullin dake hannuna ya bude min kofar motar, muna shiga ya juyar da ita muka fice.
Duk da gudun da salih keyi iya krfnsa amma na raina gudun ji nake kmr na sauka na ruga da gudu, kuka kawai nake rusawa 2n salih na bani hakuri har ya gaji ya daina.
Muna isowa harabar asibitin kukana ya karu 2n kafin ya gama tsayawa nayi ready na sauka, yana tsayawa nayi yunkurin fita yayi saurin dakatar dani da fadin "hajiya kiyi hakuri ki rage kukan nan don Allah ki samu nutsuwa ko yayane, dubi yadda kike fa!!
Nabi mayafina da takalmina wadanda duk suke rike a hannuna nabi shi da kallo kawai na saki takalmin zuwa kasa na zirashi ckn kafata na yafa mayafin akan kafata kawai nayo waje nayi saurin tsayawa sakamakon motar dana gani a nesa kadan dani na ganeta motar tasin da faruk yahau ce, gaba daya tayi raga-raga lallai ba karamin accident bane.
Nan fa na sake rudewa da firgici me tsananin, 'IHHH!!!! bakina ya furta dai-dai sanda hakorana suka fara karo na sama na dukan na kasa ji kake KAF! KAF! KAF! jikina yadau tsima.
nasan zaiyi wuya wanda ke ckn motar nan ya fita da rai, na juya da gudu izuwa ckn asibitin

bangaren Emergency na nufa don nasan bazai
wuce can ba, 2n kafin na karasa naga an fito
da wani daga daki bisa irin gadon nan da ake
2rawa an lullube jikinsa alamun ya mu2.
kawai ji nayi kafafuna sun dakata, SHIKENAN!!
ya mutu!!
kukana ya canja salo, da sauri na tari gaban
wadanda ke 2ra dan siririn gadon na dire a
gabansa tare da bude mayafin dake rufe da
fuskarsa.
Nadan yi baya a zaune KAI! ba faruk bane!! na
ganeshi direban tasin ne.
Nayi wata juyawa a haka na mike tsaye da
gudu na doshi dayan dakin dake kusa da
wanda naga an fito da wancan.
Kai tsaye na fada da yake dakin nada zurfi
zarcewa nayi zuwa tsakiyarsa, tfyt tayi saurin
cnjw na koma tfy a hankali sabanin gudun da
nake yi a baya.
Har na karaso gbn gadon da yake kwance,
kwance yake idonsa a rufe tamkar meyin barci
gaba dayan kansa na nade da farin bandeji,
hannunsa dama kafarsa.
Numfashinsa na hawa da sauka a hankali, y'ar
farar kyakykyawar fuskarsa na klln sama.
Na tsaya akan gadon nasa na zuba masa ido
da yanayin da yake ciki, nabi pipe na ledar
karin jinin dake jone a jikinsa da kallo sama
inda take rataye.
Wasu hawaye da suka banbanta da nadaa
suka zubo min, Bai mutu ba.
Abinda na baiwa kaina tbbs kenan.
Na cake gwiwoyina a kasa na dora kaina bisa
